۞ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَبَ عَلَى ٱللَّهِ وَكَذَّبَ بِٱلصِّدْقِ
إِذْ جَآءَهُۥٓ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ٣٢ وَٱلَّذِى
جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ ۙ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ٣٣
لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمْ ۚ ذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْمُحْسِنِينَ ٣٤
لِيُكَفِّرَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ أَسْوَأَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ وَيَجْزِيَهُمْ أَجْرَهُم
بِأَحْسَنِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ٣٥ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِكَافٍ
عَبْدَهُۥ ۖ وَيُخَوِّفُونَكَ بِٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ
فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ٣٦ وَمَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن مُّضِلٍّ ۗ
أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِعَزِيزٍ ذِى ٱنتِقَامٍ ٣٧ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنْ أَرَادَنِىَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَٰشِفَٰتُ
ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِى بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ مُمْسِكَٰتُ رَحْمَتِهِۦ ۚ
قُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ ۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ٣٨ قُلْ يَٰقَوْمِ
ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ إِنِّى عَٰمِلٌ ۖ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ٣٩
مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيْهِ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ٤٠



**(32) Babu wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya danganawa Allah abin da bai dace da shi ba, na abokin tarayya, ko mata, ko xa. babu wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya qaryata wahayin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi. Ashe a cikin wuta babu masauki ko wurin zama ga masu kafircewa Allah, da saqon da Manzonsa ya zo da shi? tabbas suna da wurin zama da masauki a cikinta.**

**Yayin da Allah ya ambaci maqaryaci mai qaryatawa sai kuma ya ambaci mai gaskiya da gasgatawa ya ce: (33) Wanda ya zo da gaskiya a cikin maganganunsa da ayyukansa, daga cikin Annabawa da wasunsu, kuma ya gasgata da shi yana mai yin imani da shi, kuma ya yi aiki da abin da ya nuna, lallai waxannan su ne muminai na haqiqa, Waxanda suke kamanta umarnin Ubangijinsu, suke nisantar hane-hanensa.**

**(34) Suna da duk abin da ransu take so a wurin Ubangijinsu, na kayan daxi dauwamammu, wannan shi ne sakamakon masu kyautata ayyukansu tare da Mahaliccinsu da kuma bayinsa.**

**(35) Domin Allah ya kankare musu mafi munin abin da suka kasance suna aikatawa a duniya na savo, saboda tubansu da komawarsu ga Ubangijinsu, kuma ya saka musu da lada mafi kyau daga abin da suka kasance suna aikatawa na ayyukan qwarai.**

**(36) Ashe Allah bai ishi bawansa Muhammad a cikin lamarin duniyarsa da lahirarsa ba, da ba shi kariya daga maqiyansa? Haka ne, tabbas wallahi ya ishe shi. Suna tsoratar da kai ya kai wannan Manzo da gumakan su waxanda suke bautawa koma bayan Allah, wai zasu shafe ka da wani mummunan abu, saboda jahilcinsu da wautarsu. Duk wanda Allah ya tavar da shi, bai datar da shi ga shiriya ba, to babu wani mai shiriyar da zai shiryar da shi.**

**(37) Kuma duk wanda Allah ya datar da shi ga shiriya to babu wani mai vatarwa da zai iya vatar da shi. Ashe Allah ba Mabuwayi ba ne, babu wanda zai yi galaba a kansa ba, kuma mai damqar wanda ya kafirce masa ya sava masa?. Tabbas haka ne shi Mabuwayi ne, Ma'abocin damqa.**

**(38) Kuma idan ka tambayi waxannan mushirikai - Ya kai wannan Manzo -: "Wane ne ya halicci sammai da qassai ?" Wallahi zasu ce Allah ne ya halicce su, to ka gaya musu kana mai bayyana gajiyawar allolinsu: "Ku bani labarin waxannan gumakan da kuke bautawa ba Allah ba, In Allah ya yi nufin ya shafe ni da wata cuta, shin zasu iya gusar da cutarwarsa daga gare ni?. ko kuma idan Ubangijina ya nufe ni da rahama daga gare shi, shin zasu iya hana rahamarsa daga gare ni? Ka ce da su: "Allah ya isar min shi kaxai, gare shi kaxai na dogara cikin dukkan al'amura na, kuma gare shi kaxai masu dogaro suke dogara.**

**(39) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ya ku mutane na, ku yi ci gaba da aiki a kan abin da kuka yarda da shi na shirka da Allah, kuma nima zan ci gaba da abin da Ubangijina ya umarce ni da shi, na kira zuwa ga kaxaita Allah, da tsarkake ibada gare shi, da sannu zaku san qarshen kowace hanya.**

**(40) Da sannu zaku san wane ne azaba zata zo masa tun daga nan duniya, ta qasqanta shi, da wulaqanta shi, a lahira kuma azaba daumammiya ta sauka a kansa, wadda bata yankewa, kuma bata gushewa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Girman haxarin yi wa Allah qarya, da dangana masa abin da bai dace da shi ba, ko da shari'arsa Maxaukakin sarki.**

**2 - Ya tabbata Allah ya kare Manzonsa daga maqiyansa wajen su cutar da shi.**

**3 - Tabbatar da tauhidin rububiyya kaxai, ba tare da tabbatar da tauhidin Uluhiyya ba, baya kuvutar da ma'abocinsa daga azabar wuta.**

إِنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ لِلنَّاسِ بِٱلۡحَقِّۖ فَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ
فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيۡهَاۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم
بِوَكِيلٍ ٤١ ٱللَّهُ يَتَوَفَّى ٱلۡأَنفُسَ حِينَ مَوۡتِهَا وَٱلَّتِي
لَمۡ تَمُتۡ فِي مَنَامِهَاۖ فَيُمۡسِكُ ٱلَّتِي قَضَىٰ عَلَيۡهَا ٱلۡمَوۡتَ
وَيُرۡسِلُ ٱلۡأُخۡرَىٰٓ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّىۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ
يَتَفَكَّرُونَ ٤٢ أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُفَعَآءَۚ قُلۡ
أَوَلَوۡ كَانُواْ لَا يَمۡلِكُونَ شَيۡـٔٗا وَلَا يَعۡقِلُونَ ٤٣ قُل
لِّلَّهِ ٱلشَّفَٰعَةُ جَمِيعٗاۖ لَّهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ ثُمَّ
إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٤٤ وَإِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَحۡدَهُ ٱشۡمَأَزَّتۡ
قُلُوبُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِۖ وَإِذَا ذُكِرَ ٱلَّذِينَ مِن
دُونِهِۦٓ إِذَا هُمۡ يَسۡتَبۡشِرُونَ ٤٥ قُلِ ٱللَّهُمَّ فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِ عَٰلِمَ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ أَنتَ تَحۡكُمُ بَيۡنَ عِبَادِكَ
فِي مَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٤٦ وَلَوۡ أَنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَا فِي
ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا وَمِثۡلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفۡتَدَوۡاْ بِهِۦ مِن سُوٓءِ ٱلۡعَذَابِ
يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَبَدَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مَا لَمۡ يَكُونُواْ يَحۡتَسِبُونَ ٤٧



**(41) Haqiqa mu mun saukar maka da Alqur'ani bisa gaskiya, domin ka yiwa mutane gargaxi. Duk wanda ya shiryu to amfanin shiriyar gare shi zai koma, domin shiriyarsa ba zata amfani Allah ba, saboda shi mawadaci ne daga barin ta, haka kuma duk wanda ya vace to cutarwar vatansa kansa zata koma, saboda Allah (S.W.T) ba zai cutu da vatansa ba, kuma kai ba a wakiltaka ka zama mai tilasta musu shiriya ba, babu abin da yake kanka sai isar da saqon da aka umarce ka da isarwa.**

**(42) Allah ne yake karvar rayuka a lokacin da ajalinta ya cika, kuma shi ne yake karvar rayukan da ajalinsu bai cika ba a yayin barci, sai ya riqe waxanda ya yanke musu hukuncin mutuwa, ya saki waxanda bai yanke musu hukuncin mutuwar ba zuwa wani wa'adi da shi ne ya san shi, tabbas a cikin wannan karvar rai, da sakinta, da kashewa, da rayawa, akwai dalilai ga mutanen da suke tunanin cewa wanda yake aikata haka mai iko ne akan ya tashi mutane bayan sun mutu, don yi musu hisabi da bada sakamako.**

**(43) Lallai mushirikai sun riqi gumakansu su zama masu ceto a gare su koma bayan Allah, suna kwaxayin amfani daga wajensu koma bayan Allah. Ka faxa musu - Ya kai wannan Manzo -: "Yanzu kwa riqe su masu ceto koda kuwa basa mallakawa kansu da ku wani amfani? Kuma ko da basu da hankali?. Su daskararru ne, basa yin Magana, basa ji, basa gani, basa amfanarwa, basa cutarwa.**

**(44) Ka cewa waxannan mushirikai - Ya kai wannan Manzo - : "Ceto duka na Allah ne, babu wanda ya isa ya yi ceto sai da izininsa, kuma ba za a ceci kowa ba sai wanda aka yarda da shi, mulkin sammai da mulkin qassai duk na Allah ne shi kaxai, kuma gare shi ne kaxai za a komar da ku ranar alqiyama, domin yi muku hisabi da sakamako, sai ya saka muku a kan ayyukan ku.**

**(45) Idan aka ambaci Allah shi kaxai sai zukatan mushirikai, waxanda ba su yi imani da ranar lahira da abin da yake cikinta na tashi bayan mutuwa, da hisabi, da sakamako ba, su qyamaci ambaton Allah, amma idan aka ambaci gumakan da suke bauta masu koma bayan Allah, sai ka ga suna ta yin farin ciki da walwala.**

**(46) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ya Allah Mahaliccin sammai da qassai, ba tare da ya ga samfur a wurin wani ba. Masanin abin da ke voye da bayyane, babu abin da yake vuya a gareka, kai kaxai ne kake rarrabewa a tsakanin bayinka ranar alqiyama, cikin abin da suka kasance suna yin savani a duniya, kuma sai ka bayyana mai gaskiya daga maras gaskiya, xan-Aljannah da xan wuta.**

**(47) Da a ce waxanda suka zalunci kansu da yin shirka da savon Allah, suna mallakar abin da yake cikin duniya na dukiya mai tsada, to da sun fanshi kansu daga azaba mai tsanani, wadda suka gan ta bayan tashin su daga mutuwa, sai dai lamarin ba haka yake ba, kuma da a ce suna da damar to da ba za a karva daga gare su ba. Ire-iren azaba daga Allah wadda ba sa tsammani ta bayyana a gare su.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Barci da farkawa darussa ne guda biyu, na yau da kullum da suke tunatar da mu mutuwa da tashi daga mutuwar.**

**2 - Idan aka ambaci Allah shi kaxai a wurin kafirai sai qunci da damuwa su same su, domin suna tuna umarni da hani da aka yi musu, alhali kuma sun basu baya.**

**3 - Qoqarin kafiri na ya fanshi kansa ranar alqiyama da duk abin da yake mallaka, tare da cewa a duniya shi mai tsananin rowa ne, kuma koda zai bayar ba za a karva daga gare shi ba.**

وَبَدَا لَهُمْ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُوا۟ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ
يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٤٨﴾ فَإِذَا مَسَّ ٱلْإِنسَـٰنَ ضُرٌّ دَعَانَا ثُمَّ إِذَا خَوَّلْنَـٰهُ
نِعْمَةً مِّنَّا قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلْمٍۭ ۚ بَلْ هِىَ فِتْنَةٌ وَلَـٰكِنَّ
أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٩﴾ قَدْ قَالَهَا ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَمَآ
أَغْنَىٰ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿٥٠﴾ فَأَصَابَهُمْ سَيِّـَٔاتُ
مَا كَسَبُوا۟ ۚ وَٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مِنْ هَـٰٓؤُلَآءِ سَيُصِيبُهُمْ سَيِّـَٔاتُ
مَا كَسَبُوا۟ وَمَا هُم بِمُعْجِزِينَ ﴿٥١﴾ أَوَلَمْ يَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ
ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَـٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ
﴿٥٢﴾ ۞ قُلْ يَـٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ أَسْرَفُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُوا۟ (ربع الحزب ٤٧)
مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُۥ هُوَ
ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٣﴾ وَأَنِيبُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَأَسْلِمُوا۟ لَهُۥ مِن
قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ﴿٥٤﴾ وَٱتَّبِعُوٓا۟ أَحْسَنَ
مَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِيَكُمُ ٱلْعَذَابُ
بَغْتَةً وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٥٥﴾ أَن تَقُولَ نَفْسٌ يَـٰحَسْرَتَىٰ
عَلَىٰ مَا فَرَّطتُ فِى جَنۢبِ ٱللَّهِ وَإِن كُنتُ لَمِنَ ٱلسَّـٰخِرِينَ ﴿٥٦﴾



**(48) Miyagun ayyukan da suka aikata na shirka da savo suka bayyana a gare su, azaba ta kewaye su, wadda a duniya idan aka tsoratar da su ita suke yin izgili da ita.**

**(49) Idan rashin lafiya ko talauci ko makamancinsu suka samu kafiri, sai ya kira mu, don mu yaye masa abin da ya same shi, sannan kuma idan muka ba shi wata ni'ima ta lafiya ko dukiya sai kafirin ya ce: "Kaxai Allah ya ba ni wannan ne saboda ya san na cancanta". Amma maganar gaskiya wannan jarrabawa ce da kuma talala, sai dai mafi yawan kafirai basu san hakan ba, sai kaga suna ruxuwa da ni'imar da Allah ya yi musu.**

**(50) Haqiqa Kafirai a gabaninsu sun faxi irin wannan magana, abin da suke tarawa na dukiya da matsayi bai amfana musu komai ba.**

**(51) Sakamakon mummunan aikinsu na shirka da savon Allah ya same su. Waxanda suka zalunci kansu da shirka da savo cikin waxannan da suke nan, su ma sakamakon miyagun ayyukansu zasu same su, kamar yadda suka samu waxanda suka wuce, ba zasu tserewa Allah ko su rinjaye shi ba.**

**(52) Shin waxannan mushirikai sun faxi abin da suka faxa ne, saboda ba su san Allah yana yalwata arzikinsa ga wanda ya ga dama ba, don ya jarabe shi, shin zai gode ko zai butulce? Kuma yana quntata shi ga wanda ya ga dama, don ya jarraba shi, shin zai zai yi haquri, ko zai yi fushi da qaddarar Allah?. Lallai a cikin wannan abin da aka ambata akwai dalilai da suke nuna gudanarwar Allah ga mutane masu imani, domin su ne kaxai suke amfanuwa da dalilai. Amma su kafirai suna wuce waxannan dalilai, suna masu bijire musu.**

**(53) Ya kai wannan Manzon ka cewa bayina waxanda suka qetare iyaka da yin shirka da savo: "Kada ku xebe qauna daga rahamar Allah da gafararsa ga zunubanku, tabbas Allah yana gafarta zunuban wanda ya tuba zuwa gare shi gaba xayan su. Lallai shi mai yawan gafara ne ga zunuban masu tuba, kuma mai jin qan su ne.**

**(54) Ko koma ga Ubangijinku da tuba da ayyuka na qwarai, ku jayu zuwa gare shi, tun gabanin azabar ranar alqiyama ta zo muku, sannan ba zaku samu wanda zai iya taimaka muku a cikin gumakan ku ko iyalanku, ballantana ya tseratar da ku daga azaba.**

**(55) Ku bi Alqur'ani, wanda shi ne mafi kyan abin da Ubangijinku ya saukarwa Manzonsa, ku yi aiki da umarninsa, kuma ku nisanci hane-hanensa, tun gabanin azaba ta zo muku ba tsammani, ballantana ku yi mata shiri ku tuba.**

**(56) Ku aikata hakan don gudun kada wata rai saboda da na sani ranar alqiyama ta ce: "Kaiconta da irin sakacin da ta yi wurin biyayya ga Allah, saboda abin da take kai na kafirci da savon Allah, da yin izgili ga masu imani da biyayya ga Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ni'ima ga kafiri talala ce aka yi masa.**
**2 - Yalwar rahamar Allah ga bayinsa.**
**3 - Nadama mai amfani ita ce wadda aka yi ta a duniya, kuma tuba na gaskiya ya biyo bayan ta.**

أَوۡ تَقُولَ لَوۡ أَنَّ ٱللَّهَ هَدَىٰنِي لَكُنتُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٥٧ أَوۡ تَقُولَ
حِينَ تَرَى ٱلۡعَذَابَ لَوۡ أَنَّ لِي كَرَّةٗ فَأَكُونَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ
٥٨ بَلَىٰ قَدۡ جَآءَتۡكَ ءَايَٰتِي فَكَذَّبۡتَ بِهَا وَٱسۡتَكۡبَرۡتَ وَكُنتَ
مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٩ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ تَرَى ٱلَّذِينَ كَذَبُواْ عَلَى
ٱللَّهِ وُجُوهُهُم مُّسۡوَدَّةٌۚ أَلَيۡسَ فِي جَهَنَّمَ مَثۡوٗى لِّلۡمُتَكَبِّرِينَ
٦٠ وَيُنَجِّي ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ بِمَفَازَتِهِمۡ لَا يَمَسُّهُمُ ٱلسُّوٓءُ
وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٦١ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ
شَيۡءٖ وَكِيلٞ ٦٢ لَّهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٦٣ قُلۡ
أَفَغَيۡرَ ٱللَّهِ تَأۡمُرُوٓنِّيٓ أَعۡبُدُ أَيُّهَا ٱلۡجَٰهِلُونَ ٦٤ وَلَقَدۡ
أُوحِيَ إِلَيۡكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكَ لَئِنۡ أَشۡرَكۡتَ
لَيَحۡبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٦٥ بَلِ
ٱللَّهَ فَٱعۡبُدۡ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ٦٦ وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ
قَدۡرِهِۦ وَٱلۡأَرۡضُ جَمِيعٗا قَبۡضَتُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ
مَطۡوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٧



**(57) Ko kuma ta kafa hujja da qaddara ta ce: “Da ace Allah ya datar da ni ga shiriya da na zama cikin masu tsoronsa, ina kamanta umarninsa, ina nisantar haninsa”.**

**(58) Ko kuma ta ce a lokacin da ta yi ido biyu da azaba tana mai buri: “Ina ma dai a ba ni damar komawa duniya sai na tuba ga Allah, na kasance cikin masu kyautata ayyukansu”.**

**(59) Lamarin da sha’anin sam ba kamar yadda kake riyawa ba ne a kan shiriya, ayoyi na sun zo maka, amma sai ka qaryata, ka yi girman kai, ka zamo daga cikin waxanda suke kafircewa Allah da ayoyinsa, da Manzannin sa.**

**(60) A ranar alqiyama zaka ga waxanda suka yi wa Allah qarya, ta hanyar jingina masa abokin tarayya, ko xa, fuskokinsu sun yi baqi, alamar da take nuna tavewarsu. Ashe a cikin wutar Jahannama babu matabbata ga masu girman kai ga barin imani da Allah da Manzanninsa ba? Tabbas akwai, a cikinta akwai matabbatarsu.**

**(61) Kuma Allah zai kuvutar da waxanda suka ji tsoron Ubangijinsu, suka kamanta umarnin sa, suka nisanci hane hanensa daga azaba, ta hanyar shigar da su gidan rabautarsu, shi ne Aljannah, wata azaba ba zata same su ba, kuma ba zasu yi baqin ciki ba dangane da abin da ya kuvuce musu na rabon a duniya.**

**(62) Allah ne ya halicci komai, babu wani mahalicci ba shi ba, kuma shi mai kiyaye wa ne a kan komai, shi ne yake gudanar da al’amuransa, ya sarrafa shi yadda ya ga dama.**

**(63) A wurinsa ne kaxai mabuxan dukkan alheri suke, a cikin sammai da qassai, yana bada su ga wanda ya ga dama, kuma ya hana wanda ya ga dama. Waxanda suka kafirce wa ayoyin Allah, waxannan su ne asararru, don sun rasa imani a rayuwar su ta duniya, da shigar su wuta a ranar alqiyama, suna masu dauwama a cikinta ranar alqiyma.**

**(64) Ka cewa waxannan mushirikai da suke neman ka bautawa gumakansu - Ya kai wannan Manzo -: “Ya ku waxanda kuka jahilci Ubangijinku shin kuna umarta ta ne in bautawa wanin Allah?. Babu wanda ya cancanci bauta sai Allah shi kaxai. Don haka ba zan bautawa waninsa ba”.**

**(65) Haqiqa Allah ya yi wahayi gare ka - Ya kai wannan Manzo – kuma an yi wahayi ga Annabawan da suka gabace ka cewa: “Idan ka bautawa wani tare da Allah, to lallai zaka vata ayyukanka na qwarai, kuma lallai zaka zama daga cikin masu asara a duniya, ta hanyar asarar addininka, a lahira kuma ka gamu da azaba”.**

**(66) Kawai ka bautawa Allah shi kaxai, kada ka haxa shi da kowa, kuma kasance cikin masu godiya ga ni’imar da ya yi maka.**

**(67) Mushirikai basu girmama Allah ba girmamawar da ta dace da shi, a yayin da suka haxa shi wajen bauta da halittarsa masu rauni gajiyayyu, suka rafkana daga ikon Allah, wanda daga cikin alamunsa qasa da abin da yake bayanta na duwatsu da bishiyoyi da tekuna da qoramu, duk suna cikin damqarsa ranar alqiyama, haka nan sammai guda bakwai dukkaninsu ababen naxewa ne a damansa. Allah ya girmama, ya tsarkaka, ya xaukaka daga dukkan abin da mushirikai suke faxa kuma suke qudirewa game da shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Girman kai xabi’a ce mummuna, tana hana a gane gaskiya.**
**2 - Duhun fuskoki a ranar alqiyama, alama ce ta tavewar masu ita.**
**3 - Shirka tana rusa dukkan ayyuka nagari.**
**4 - Tabbatar siffar damqa da hannun dama ga Allah Maxaukakin sarki, ba tare da kamantawa ko misaltawa ba.**

وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ
إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۖ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخۡرَىٰ فَإِذَا هُمۡ قِيَامٞ يَنظُرُونَ
٦٨ وَأَشۡرَقَتِ ٱلۡأَرۡضُ بِنُورِ رَبِّهَا وَوُضِعَ ٱلۡكِتَٰبُ وَجِاْيٓءَ
بِٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَقُضِيَ بَيۡنَهُم بِٱلۡحَقِّ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ
٦٩ وَوُفِّيَتۡ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا عَمِلَتۡ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٧٠
وَسِيقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا
فُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَآ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ
يَتۡلُونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِ رَبِّكُمۡ وَيُنذِرُونَكُمۡ لِقَآءَ يَوۡمِكُمۡ
هَٰذَاۚ قَالُواْ بَلَىٰ وَلَٰكِنۡ حَقَّتۡ كَلِمَةُ ٱلۡعَذَابِ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ
٧١ قِيلَ ٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئۡسَ مَثۡوَى
ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ٧٢ وَسِيقَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ إِلَى ٱلۡجَنَّةِ
زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَا
سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡ طِبۡتُمۡ فَٱدۡخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ٧٣ وَقَالُواْ
ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي صَدَقَنَا وَعۡدَهُۥ وَأَوۡرَثَنَا ٱلۡأَرۡضَ
نَتَبَوَّأُ مِنَ ٱلۡجَنَّةِ حَيۡثُ نَشَآءُۖ فَنِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ٧٤



**(68) Ranar da Mala'ikan da aka wakilta da yin busa a qaho ya yi busa, to duk wanda yake cikin sammai da qassai sai ya mutu, sannan sai Mala'ikan ya sake yin wata busa ta biyu, don tashi bayan mutuwa, sai ka ga dukkan rayayyu sun tashi suna sauraron me Allah zai yi da su.**

**(69) Kuma qasa ta yi haske saboda bayyanar Ubangiji don yin hukunci a tsakanin bayi. Aka watsa takardun ayyukan mutane, aka zo da Annabawa, A ka zo da al'ummar Annabi Muhammad (S.A.W) don ta yi wa Annabawa shaida a kan mutanensu, Allah ya yi hukunci a tsakanin kowa da adalci, baza a zaluncesu ba a wannan rana, ba za a qarawa mutum mummunan aiki ba, kuma ba za a rage masa kyakkyawan aiki ba.**

**(70) Allah ya kammala sakamakon kowace rai, alheri ne aikinta ko sharri ne. Allah ne ya fi kowa sanin abin da suke aikata, babu abin da yake vuya a gare shi na ayyukansu, alheri ne ko sharri, kuma akan ayyukansu zai yi musu sakayya a wannan rana.**

**(71) Mala'iku suka koro waxanda suka kafirce wa Allah zuwa wutar Jahannama, jama'a da yawa a cikin qasqanci, har sai idan sun zo Jahannama sai Mala'iku masu gadinta su buxe musu qofofinta, su tare su da wulaqantawa, su ce musu: " Manzanni daga jinsinku basu zo muku ba ne, suna karanta muku ayoyin Ubangijinku waxanda aka saukar musu, suna tsoratar da ku haxuwa da ranar alqiyama ba, saboda abin da yake cikin ranar na azaba mai tsanani?. Sai waxanda suka yi kafirci su ce, suna masu tabbatar da hakan: " Gaskiya ne, duk abin da kuka faxa ya faru, sai dai kawai azaba ta tabbata ga kafirai, mu kuma mun kasance daga cikin kafirai.**

**(72) Sai a ce da su cikin wulaqantar wa da xebe musu qauna daga rahamar Allah, da xebe musu qauna daga fitowa daga wuta: "Ku shiga qofofin wutar Jahannama, kuna masu zama a cikinta har abada. Matabbatar masu girman kai, masu qin gaskiya ta munana.**

**(73) Mala'iku zasu rako muminai masu tsoron, waxanda suke kamanta umarnin Allah suke nisantar abubuwan da ya hana zuwa ga Aljannah, cikin tawaga abar girmamawa, har sai sun zo Aljannah sai a buxe musu qofofinta, kuma sai Mala'iku masu kula da ita su ce musu: "Aminci ya tabbata a gare ku daga dukkan abin da kuke qi, zukatanku sun kyautata da ayyukan ku, ku shiga cikin Aljannah, ku masu zama a cikinta har abada.**

**(74) Yayin da muminai suka shiga Aljannah sai su ce: "Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya gasgata mana alqawarin da ya yi mana a bisa harshen manzanninsa, ya yi mana alqawarin zai shigar damu Aljannah, kuma ya gadar mana da gidan Aljannah, muna sauka a wurin da muka ga dama, madallah da ladan masu yin aiki, waxanda su ke yin aiki na qwarai domin neman yardar Ubangijinsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Busa guda biyu a qaho tabbatattu ne.**
**2 - Bayanin wulaqantar da kafirai zasu gamu da ita, da kuma irin girmamawar da za a tari muminai da ita.**
**3 - Tabbatar da dauwamar kafirai a cikin jahima, da dauwamar muminai a cikin ni'ima.**
**4 - Kyakkyawan aiki yana gadar da kyakkyawan sakamako.**

وَتَرَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ حَآفِّينَ مِنْ حَوْلِ ٱلْعَرْشِ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ
رَبِّهِمْ ۖ وَقُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْحَقِّ ۚ وَقِيلَ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٧٥

سُورَةُ غَافِرٍ — ترتيبها ٤٠ — آياتها ٨٥

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ١ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْعَلِيمِ ٢ غَافِرِ ٱلذَّنۢبِ
وَقَابِلِ ٱلتَّوْبِ شَدِيدِ ٱلْعِقَابِ ذِى ٱلطَّوْلِ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ إِلَيْهِ
ٱلْمَصِيرُ ٣ مَا يُجَٰدِلُ فِىٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فَلَا يَغْرُرْكَ
تَقَلُّبُهُمْ فِى ٱلْبِلَٰدِ ٤ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَٱلْأَحْزَابُ
مِنۢ بَعْدِهِمْ ۖ وَهَمَّتْ كُلُّ أُمَّةٍۭ بِرَسُولِهِمْ لِيَأْخُذُوهُ ۖ
وَجَٰدَلُوا۟ بِٱلْبَٰطِلِ لِيُدْحِضُوا۟ بِهِ ٱلْحَقَّ فَأَخَذْتُهُمْ ۖ فَكَيْفَ
كَانَ عِقَابِ ٥ وَكَذَٰلِكَ حَقَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ
كَفَرُوٓا۟ أَنَّهُمْ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ٦ ٱلَّذِينَ يَحْمِلُونَ ٱلْعَرْشَ
وَمَنْ حَوْلَهُۥ يُسَبِّحُونَ بِحَمْدِ رَبِّهِمْ وَيُؤْمِنُونَ بِهِۦ وَيَسْتَغْفِرُونَ
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۖ رَبَّنَا وَسِعْتَ كُلَّ شَىْءٍ رَّحْمَةً وَعِلْمًا فَٱغْفِرْ
لِلَّذِينَ تَابُوا۟ وَٱتَّبَعُوا۟ سَبِيلَكَ وَقِهِمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ٧



**(75) Kuma Mala'iku zasu kasance a wannan rana abar halarta, suna kewaye da al'arshin Allah, suna tsarkake shi daga abin da bai dace da shi ba, na daga maganganun kafirai. Allah ya yi hukunci a tsakanin bayi da adalci, ya girmama wanda ya girmama, ya azabtar da wanda ya azabtar. Aka ce: "Yabo da kirari da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halittu, a kan hukuncinsa da abin da ya yi hukunci da shi, na jinqai ga bayinsa muminai, daa azbtar da bayinsa kafirai.**

# Suratu Gafir

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Magance matsalar masu jayayya da ayoyin Allah ta hanyar tattaunawa da su, da kuma yin muhawara, da kiransu domin su dawo ga gaskiya.**

## Tafsir:

**(1) (Haa mim) Bayani akan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon a farkon suratul baqarah.**

**(2) Saukar da Alqur'ani wanda aka saukar ga Annabi Muhammad (S.A.W) daga Allah ne, Mabuwayi, wanda babu mai rinjayarsa, kuma masanin masalahar bayinsa.**

**(3) Mai gafarta zunuban masu zunubi ne, mai karvar tuban wanda ya tuba zuwa gare shi daga cikin bayinsa, mai tsananin uquba ne ga wanda bai tuba daga zunubansa ba ne. Ma'abocin kyautatawa da karamci ne. Babu wani abin bautawa da gaskiya wanda ba shi ba, makomar bayi zuwa gare shi ne kaxai za ta kasance, a ranar alqiyama, sai ya saka musu da abin da suka cancance shi.**

**(4) Babu mai yin jayayya da ayoyin Allah, waxanda suke nuna kaxaitakarsa, da gaskiyar Manzonsa sai waxanda suka kafirce wa Allah, saboda vacewar hankulansu, don haka kada ka yi baqin ciki a kansu, kuma kada abin da suke ciki na yalwa da arziki ya ruxe ka, jinkirta musu talala ce gare su.**

**(5) Gabanin waxannan mutanen Annabi Nuhu sun qaryata, haka ma qungiyoyi da suka zo a bayansa su ma sun qaryata, Adawa sun qaryata, Samudawa ma haka, da mutanen Annabi Luxu, da mutanen Madyana, Fir'auna ma ya qaryata, kowace al'umma daga cikin al'ummai ta yi nufin ta kama Manzonta ta kashe shi, suka yi jayayya a kan abin da suke kai na varna, don su kawar da gaskiya da shi, sai na kama dukkan waxannan al'ummu, ka lura yaya uqubata ta kasance a kansu, tabbas ta kasance uquba mai tsanani.**

**(6) To kamar yadda Allah ya yanke hukuncin halakarwa ga al'ummun can gaba xaya, haka kalmar Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo ta tabbata a kan kafirai cewa su yan wuta ne.**

**(7) Mala'ikun da suke xauke da al'arshin Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - da waxanda suke kewaye da shi, suna tsarkake Ubangijinsu ga barin abin da bai dace da shi ba, kuma suna yin imani da shi, suna nema wa Muminai gafara, suna cewa a cikin addu'arsu: "Ya Ubangijinmu, iliminka da rahamarka sun yalwaci komai, ka gafarta wa waxanda suka tuba daga laifukansu, kuma suka bi addininka, ka kiyaye su daga wuta kada ta shafe su".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Haxawa tsakanin kwaxaitarwa ga rahamar Allah, da tsoratarwa ga tsananin uqubarsa, yin hakan salo ne mai kyau.**

**2 - Yabo ga Allah ta hanyar kaxaita shi, da tsarkake shi, tare da yi masa godiya, hakan ladabi ne cikin ladubban addu'a.**

**3 - Girman mumini a wurin Allah, ta inda ya hore masa Mala'iku don su riqa nema masa gafara.**

رَبَّنَا وَأَدۡخِلۡهُمۡ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدتَّهُمۡ وَمَن صَلَحَ
مِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَأَزۡوَٰجِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ
ٱلۡحَكِيمُ ٨ وَقِهِمُ ٱلسَّيِّـَٔاتِۚ وَمَن تَقِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ
يَوۡمَئِذٖ فَقَدۡ رَحِمۡتَهُۥۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٩ إِنَّ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُنَادَوۡنَ لَمَقۡتُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُ مِن مَّقۡتِكُمۡ
أَنفُسَكُمۡ إِذۡ تُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلۡإِيمَٰنِ فَتَكۡفُرُونَ ١٠ قَالُواْ رَبَّنَآ
أَمَتَّنَا ٱثۡنَتَيۡنِ وَأَحۡيَيۡتَنَا ٱثۡنَتَيۡنِ فَٱعۡتَرَفۡنَا بِذُنُوبِنَا فَهَلۡ
إِلَىٰ خُرُوجٖ مِّن سَبِيلٖ ١١ ذَٰلِكُم بِأَنَّهُۥٓ إِذَا دُعِيَ ٱللَّهُ
وَحۡدَهُۥ كَفَرۡتُمۡ وَإِن يُشۡرَكۡ بِهِۦ تُؤۡمِنُواْۚ فَٱلۡحُكۡمُ لِلَّهِ
ٱلۡعَلِيِّ ٱلۡكَبِيرِ ١٢ هُوَ ٱلَّذِي يُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُنَزِّلُ لَكُم مِّنَ
ٱلسَّمَآءِ رِزۡقٗاۚ وَمَا يَتَذَكَّرُ إِلَّا مَن يُنِيبُ ١٣ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ
مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١٤ رَفِيعُ
ٱلدَّرَجَٰتِ ذُو ٱلۡعَرۡشِ يُلۡقِي ٱلرُّوحَ مِنۡ أَمۡرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ
مِنۡ عِبَادِهِۦ لِيُنذِرَ يَوۡمَ ٱلتَّلَاقِ ١٥ يَوۡمَ هُم بَٰرِزُونَۖ لَا يَخۡفَىٰ
عَلَى ٱللَّهِ مِنۡهُمۡ شَيۡءٞۚ لِّمَنِ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَۖ لِلَّهِ ٱلۡوَٰحِدِ ٱلۡقَهَّارِ ١٦



**(8) Kuma Mala'iku suna cewa: "Ya Ubangijin mu, ka shigar da Muminai Aljannatai na dauwama, wadda ka yi musu alqawarin zaka shigar da su cikinta, kuma ka shigar da waxanda ayyukansu suka yi kyau daga cikin iyayensu, da matayensu, da 'ya'yayensu, haqiqa kai Mabuwayi ne da babu wanda ya isa ya rinjaye ka, kuma kai mai hikima cikin tsarinka da gudanarwarka". (9) Kuma ka kiyaye su daga munanan ayyukansu, kada ka azabtar da su da ita, duk wanda ka kiyaye shi daga uqubar munanan ayyukan shi ranar alqiyama to tabbas ka jiqansa. Wannan kariya daga azaba, da kuma jinqai ta hanyar shiga Aljannah, ita ce babban rabon da babu rabon da ya ka shi. (10) Haqiqa waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa, za a kirawo su ranar alqiyama a lokacin da zasu shiga wuta, suna masu jin haushin kawunansu da la'antarta, za a ce musu: "Tsananin qiyayyar da Allah yake yi muku ya fi tsanin qiyayyar da kuke yi wa kawunanku, a lokacin da ake kiran ku a duniya domin ku yi imani da Allah, amma sai kuka kafirce masa, kuka riqi wasu alloli a tare da shi".**

**(11) Kafirai zasu ce, suna masu tabbatar da laifukansu, a lokacin da tabbatarwar su ko tubansu baza ta yi musu amfani ba,: "Ya Ubangijin mu ka kashe mu sau biyu, lokacin da babu mu sai ka samar da mu, sannan ka kashe mu bayan wannan samarwar. Ka raya mu har sau biyu, ta hanyar samar da mu daga rashi, da kuma raya mu da tashi bayan mutuwa, don haka mun yarda da laifukan mu waxanda muka aikata, to ko akwai wata hanya da zata fitar da mu daga wuta, mu koma rayuwar duniya domin mu gyara ayyukanmu, ko ka yarda da mu?". (12) Wannan azabar da aka azabatar da ku da ita, saboda kun kasance idan aka kira Allah shi kaxai, ba a yi shirka da shi ba, sai ku kafirce masa, ku sanya masa abokan tarayya, amma idan aka bautawa Allah tare da wani abokin tarayya sai ku yi imani, to hukunci na Allah shi kaxai, wanda yake Maxaukaki da zatinsa, da ikonsa, da rinjayensa, mai girman da komai qasa da shi yake.**

**(13) Allah shi ne yake nuna muku ayoyinsa a cikin duniya da kawunanku, don waxannan ayoyi su nuna muku ikon Allah da kaxaitakar sa, kuma yake saukar muku da ruwan sama, don ya zama dalilin abin da ake azurta ku da shi daga tsirrai da shuka, da sauransu. Babu wanda yake wa'azantu wa da ayoyin Allah sai mai komawa gare shi da tuba, da tsarkake zuciya.**

**(14) Ku kira Allah – Ya ku Muminai - kuna masu tsarkake xa'a da kira zuwa gare shi, ka da haxa shi da wani, koda kafirai sun qi haka, kuma hakan yana sa su ji haushi.**

**(15) Domin Allah shi ne ya cancanta a tsarkake shi da xa'a da addu'a, shi ne mai maxaukakiyar daraja, wanda baya cakuxe da bayinsa, shi ne Ubangijin al'arshi mai girma, yana saukar da wahayi ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, don ya raya su, su kuma su raya wasun su, kuma don su tsoratar da mutane ranar alqiyama, ranar da mutanen farko da na qarshe za su haxu.**

**(16) A ranar zasu bayyana, su taru a fili xaya, babu wani abu nasu da yake vuya ga Allah, zatinsu ne ko ayyukansu ko sakamakon su, kuma za a tambaye su a ce da su: "Yau mulki na wane ne?" A lokacin babu wata amsa sai guda xaya tal, mulki na Allah ne, wanda yake shi kaxai a cikin zatinsa, da siffofinsa, da ayyukansa, kuma shi ne mai rinjaye, wanda ya rinjayi komai, kuma dukkan komai ya sunkuya gare shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - A duniya ake karvar tuba kaxai. 2 - Amfanin wa'azi ya kevanta ne ga masu komawa ga Ubangijinsu. 3 - Qin kafirai ga addini da matakin da suke xauka baya tasiri a kan Mumini da ya tsaya a kan addini. 4 - Ranar alqiyama azzalumai da masu xagawa duk zasu ranqwafa ga Allah.**

ٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا كَسَبَتۡۚ لَا ظُلۡمَ ٱلۡيَوۡمَۚ إِنَّ
ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٧ وَأَنذِرۡهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡأٓزِفَةِ إِذِ ٱلۡقُلُوبُ
لَدَى ٱلۡحَنَاجِرِ كَٰظِمِينَۚ مَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ حَمِيمٖ وَلَا شَفِيعٖ
يُطَاعُ ١٨ يَعۡلَمُ خَآئِنَةَ ٱلۡأَعۡيُنِ وَمَا تُخۡفِي ٱلصُّدُورُ ١٩ وَٱللَّهُ
يَقۡضِي بِٱلۡحَقِّۖ وَٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَقۡضُونَ
ثلاثة أرباع الحزب ٤٧ بِشَيۡءٍۗ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ٢٠ ۞ أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي
ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ كَانُواْ مِن قَبۡلِهِمۡۚ
كَانُواْ هُمۡ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَءَاثَارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ
بِذُنُوبِهِمۡ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٖ ٢١ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ
كَانَت تَّأۡتِيهِمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَكَفَرُواْ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُۚ
إِنَّهُۥ قَوِيّٞ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢٢ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا
وَسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٍ ٢٣ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَقَٰرُونَ
فَقَالُواْ سَٰحِرٞ كَذَّابٞ ٢٤ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلۡحَقِّ مِنۡ
عِندِنَا قَالُواْ ٱقۡتُلُوٓاْ أَبۡنَآءَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ وَٱسۡتَحۡيُواْ
نِسَآءَهُمۡۚ وَمَا كَيۡدُ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ ٢٥



**17 A wannan rana ne za a sakawa kowace rai da abin da ta aikata, idan alheri ta yi ta ga alheri, idan sharri ta yi ta ga sharri, babu zalunci a wannan ranar, domin mai hukunci shi ne Allah mai adalci, kuma haqiqa Allah mai gaggawar hisabi ne ga bayinsa, saboda kiwayewar iliminsa gare su.**

**18 Ka tsoratar da su - Ya kai wannan Manzo - da ranar alqiyama, wannan alqiyamar da ta qarato, tabbas zata zo, domin duk abin da zai zo to a kusa yake. A wannan rana zukata zasu kasance daf da maqoshi, saboda tsananin razani, kuma zasu kasance cikin yin shiru sai dai waxanda Allah ya basu damar yin magana. Waxanda suka zalunci kawunansu ta hanyar shirka da savon Allah basu da wani aboki ko makusanci, ko mai ceto da za a saurare shi, idan da za a qaddara ya yi ceto.**

**19 Allah yana san abin da idanun masu satar kallo suke yi a voye, kuma ya san abin da qiraza suke voyewa, babu wani abu da yake vuya a gare shi cikin abin da aka ambata.**

**20 Allah zai yi hukunci bisa adalci, bazai cuci kowa ba ta hanyar rage masa kyawawan ayukansa, ko yi masa a qari a cikin munanan ayyukansa. Waxanda mushirikai suke bautawa koma bayan Allah baza su yi hukunci da komai ba, domin basa mallakar komai. Haqiqa Allah mai ji ne ga maganganun bayinsa, kuma mai ganin ayyukansu ne da niyyoyinsu. kuma da sannu zai yi musu sakayya a kansu.**

**21 Shin waxannan mushirikai basu yi tafiya ba ne a bayan qasa? su lura yaya qarshen al'ummun da suka qaryata gabaninsu ya kasance, haqiqa ya kasance mummunan qarshe, kuma waxannan al'ummun sun kasance masu tsananin qarfi fiye da waxannan, kuma sun yi tasiri a bayan qasa ta hanyar gine-gine irin tasirin da waxannan basu yi ba, amma tare da haka Allah ya halakar da su saboda zunubansu, kuma basu kasance suna da wani abu da zai kare su daga uqubar Allah ba.**

**22 Wannan azabar da ta same su, ta same su ne saboda manzanninsu suna zuwar musu da gamsassun hujjoji daga Allah, amma sai suka kafirce wa Allah, suka qaryata Manzanninsa, amma duk da irin qarfin da suke da shi sai da Allah ya kama su, ya halakar da su. Haqiqa shi Allah mai qarfi ne, kuma mai tsananin uquba ne ga wanda ya kafirce masa, ya qaryata Manzanninsa.**

**Yayin da Manzon Allah (S.A.W) ya fuskanci qaryatawar mutanensa, sai Allah ya ambata masa labarin Annabi Musa (A.S) da Fir'auna, don yi masa bushara da cewa qarshen lamarinsa shi ne cin nasara, Allah ya ce:**

**23 Haqiqa mun aika Annabi Musa da ayoyinmu bayyanannu, da hujja yankakkiya.**

**24 Zuwa ga Fir'auna da wazirinsa Hamana da kuma Qaruna, amma duk sai suka ce: "Musa matsafi ne, kuma maqaryaci ne a cikin da'awar da yake yi shi Manzo ne".**

**25 A lokacin da Annabi Musa ya zo da hujjojin da suke nuna gaskiyarsa, sai Fir'auna ya ce: "ku kashe 'ya'yan waxanda suka yi imani da shi, ku bar matayen su, don wulaqanci gare su, makircin kafirai na qarantar da muminai a wofi zai tafi, ba zai yi tasiri ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tunatarwa a kan tashin alqiyama yana daga cikin manya manyan abubuwa da suke razanarwa ga barin savon Allah.**

**2 - Gamewar ilimin Allah da ayyukan bayi, a voye suke ko a bayyane.**

**3 - Umarni da yin tafiya a bayan qasa, domin wa'azantuwa daga yanayin mushirikan da aka halakar.**

وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ ذَرُونِيٓ أَقۡتُلۡ مُوسَىٰ وَلۡيَدۡعُ رَبَّهُۥٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ
أَن يُبَدِّلَ دِينَكُمۡ أَوۡ أَن يُظۡهِرَ فِي ٱلۡأَرۡضِ ٱلۡفَسَادَ ٢٦
وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِنِّي عُذۡتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٖ لَّا يُؤۡمِنُ
بِيَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ ٢٧ وَقَالَ رَجُلٞ مُّؤۡمِنٞ مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ
يَكۡتُمُ إِيمَٰنَهُۥٓ أَتَقۡتُلُونَ رَجُلًا أَن يَقُولَ رَبِّيَ ٱللَّهُ وَقَدۡ
جَآءَكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ مِن رَّبِّكُمۡۖ وَإِن يَكُ كَٰذِبٗا فَعَلَيۡهِ
كَذِبُهُۥۖ وَإِن يَكُ صَادِقٗا يُصِبۡكُم بَعۡضُ ٱلَّذِي يَعِدُكُمۡۖ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ مُسۡرِفٞ كَذَّابٞ ٢٨ يَٰقَوۡمِ لَكُمُ
ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَ ظَٰهِرِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَمَن يَنصُرُنَا مِنۢ بَأۡسِ ٱللَّهِ
إِن جَآءَنَاۚ قَالَ فِرۡعَوۡنُ مَآ أُرِيكُمۡ إِلَّا مَآ أَرَىٰ وَمَآ أَهۡدِيكُمۡ
إِلَّا سَبِيلَ ٱلرَّشَادِ ٢٩ وَقَالَ ٱلَّذِيٓ ءَامَنَ يَٰقَوۡمِ إِنِّيٓ أَخَافُ
عَلَيۡكُم مِّثۡلَ يَوۡمِ ٱلۡأَحۡزَابِ ٣٠ مِثۡلَ دَأۡبِ قَوۡمِ نُوحٖ وَعَادٖ
وَثَمُودَ وَٱلَّذِينَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡۚ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلۡمٗا لِّلۡعِبَادِ ٣١
وَيَٰقَوۡمِ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ يَوۡمَ ٱلتَّنَادِ ٣٢ يَوۡمَ تُوَلُّونَ مُدۡبِرِينَ
مَا لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِنۡ عَاصِمٖۗ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٖ ٣٣



**(26) Fir'auna ya ce: "Ku rabu da ni in kashe Musa, don hakan ya zama uquba ce gare shi, shi kuma ya kira wo Ubangijinsa ya kare shi daga gare ni, ni ban damu ba ya kiran Ubangijin nasa, haqiqa ina jin tsoron kada ya canza muku addininku da kuke kai, ko kuma ya bayyana varna a bayan qasa, ta hanyar kisan kai da ta'addanci.**

**(27) Sai Annabi Musa ya ce a yayin da ya san barazanar da Fir'auna ya yi masa: "Tabbas ni na fake ga Ubangiji na kuma Ubangijinku, na yi riqo da shi, ina mai neman tsari daga dukkan wani mai girman kai ga gaskiya da imani, wanda bai yi imani da ranar tashin alqiyama, da abin da yake cikin ta na hisabi da uquba ba".**

**(28) Wani mutum mumini daga cikin mabiya Fir'auna mai voye imaninsa ga mutanensa, ya ce yana mai musu inkarin niyyarsu ta kashe Annabi Musa: "Yanzu zaku kashe mutum ba tare da wani laifi ba, sai don kawai ya ce "Allah ne Ubangijina" alhali ya zo muku da hujjoji da dalilai da suke nuna Manzancinsa daga Ubangijinsa?!. Kuma idan an qaddara ma shi maqaryaci ne, to cutar qaryarsa kansa zata koma, idan kuwa gaskiya yake, to sashen abin da yake yi muku alqawari na azaba tabbas zai same ku cikin gaggawa. Haqiqa Allah baya datar da mai qetare iyakokinsa, mai yi masa qire da Manzanninsa.**

**(29) Yaku mutane na, yau mulki naku ne, ku ne da rinjaye a qasar Masar, amma wane ne zai taimake mu daga azabar Allah idan ta zo mana, sanadiyyar kashe Annabi Musa?. Sai Fir'auna ya ce: "Ra'ayina shi ne ra'ayi, kuma hukuncina shi ne hukunci, kuma na yanke kashe Musa, domin kawar da sharri da varna, kuma babu abin da nake nuna muku face daidai da shiriya.**

**(30) Sai wanda ya yi imani ya ce, yana mai nasiha ga mutanensa: "Tabbas ina jiye muku tsoro - idan kuka kashe Musa bisa zalunci - irin narkon azabar da zai same ku, irin azabar da ta samu waxanda suka yi wa Manzannin su taron dangi, amma duk sai Allah ya halakar da su".**

**(31) Kamar al'adar waxanda suka kafirce, kuma suka qaryata Manzanni, irin mutanen Annabi Nuhu, da Adawa, da Samudawa, da waxanda suka zo a bayansu, haqiqa Allah ya halakar da su saboda kafircinsu da qaryatawar su ga Manzanni. Allah baya nufin zalunci ga bayi, kaxai yana azabtar da su ne da zunubansu, sakamakon da ya dace.**

**(32) Ya ku mutane na, ina jiye muku ranar alqiyama, ranar da mutane za su kira, sashinsu ya kira sashe, saboda kusanci dake tsakaninsu, ko wani matsayi, da tunanin cewa wannan zai yi musu wani amfani a wannan yanayi mai tsoratarwa.**

**(33) Ranar da zaku juya a guje don tsoron wuta, kuma baku da wani abu da zai kare ku daga azabar Allah. Duk wanda Allah ya wulaqantar da shi, bai datar da shi ga imani ba, to babu wani mai shiriyar da zai shiryar da shi, domin dacewa da shiriya yana hannun Allah shi kaxai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Komawar mumini ga Ubangijinsa don ya kare shi daga makircin maqiyansa.**
**2 - Halaccin voye imani domin wata masalaha mai rinjaye, ko kawar da wata varna.**
**3 - Gabatar da nasiha ga mutane yana cikin siffofin ma'abota imani.**

وَلَقَدْ جَاءَكُمْ يُوسُفُ مِن قَبْلُ بِالْبَيِّنَاتِ فَمَا زِلْتُمْ فِي
شَكٍّ مِّمَّا جَاءَكُم بِهِ حَتَّىٰ إِذَا هَلَكَ قُلْتُمْ لَن يَبْعَثَ اللَّهُ
مِن بَعْدِهِ رَسُولًا كَذَٰلِكَ يُضِلُّ اللَّهُ مَنْ هُوَ مُسْرِفٌ
مُّرْتَابٌ ٣٤ الَّذِينَ يُجَادِلُونَ فِي آيَاتِ اللَّهِ بِغَيْرِ سُلْطَانٍ
أَتَاهُمْ كَبُرَ مَقْتًا عِندَ اللَّهِ وَعِندَ الَّذِينَ آمَنُوا كَذَٰلِكَ
يَطْبَعُ اللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ قَلْبِ مُتَكَبِّرٍ جَبَّارٍ ٣٥ وَقَالَ فِرْعَوْنُ
يَا هَامَانُ ابْنِ لِي صَرْحًا لَّعَلِّي أَبْلُغُ الْأَسْبَابَ ٣٦ أَسْبَابَ
السَّمَاوَاتِ فَأَطَّلِعَ إِلَىٰ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُ كَاذِبًا
وَكَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِفِرْعَوْنَ سُوءُ عَمَلِهِ وَصُدَّ عَنِ السَّبِيلِ
وَمَا كَيْدُ فِرْعَوْنَ إِلَّا فِي تَبَابٍ ٣٧ وَقَالَ الَّذِي آمَنَ
يَا قَوْمِ اتَّبِعُونِ أَهْدِكُمْ سَبِيلَ الرَّشَادِ ٣٨ يَا قَوْمِ
إِنَّمَا هَٰذِهِ الْحَيَاةُ الدُّنْيَا مَتَاعٌ وَإِنَّ الْآخِرَةَ هِيَ
دَارُ الْقَرَارِ ٣٩ مَنْ عَمِلَ سَيِّئَةً فَلَا يُجْزَىٰ إِلَّا مِثْلَهَا
وَمَنْ عَمِلَ صَالِحًا مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُولَٰئِكَ
يَدْخُلُونَ الْجَنَّةَ يُرْزَقُونَ فِيهَا بِغَيْرِ حِسَابٍ ٤٠



**34 Haqiqa Annabi Yusuf ya zo muku tun gabanin Annabi Musa da hujjoji bayyanannu akan kaxaitakar Allah, amma baku gushe ba a cikin shakka da qaryata abin da ya zo muku da shi, har bayan ya rasu sai kuka qara samun shakka da tababa, kuka ce: "Allah ba zai qara aiko da wani Manzo ba a bayansa". To irin wannan vatan naku ga barin gaskiya, haka Allah yake vatar da duk wani mai wuce gona da iri cikin iyakokin Allah, mai shakka cikin kaxaitakarsa.**

**35 Waxanda suke jayayya cikin ayoyin Allah, domin su vata su ba tare da wata hujja ba da ta zo musu, laifin jayayyarsu ya munana a wurin Allah da wurin waxanda suka yi imani da shi da Manzanninsa. Kamar yadda Allah ya rufe zukatan waxannan masu jayayya cikin ayoyin mu domin su vata su, haka Allah yake rufe zuciyar duk mai yin girman kai ga gaskiya tare da jabberanci, kuma ba zai tava shiriya ga gaskiya ba, ba kuma zai samu shiriya zuwa ga alheri ba.**

**36 Fir'auna ya cewa wazirinsa Hamana: "Ya kai Hamana ka gina mini wani gini mai tsawo, ko na isa ga hanyoyi".**

**37 "Ko na samu isa ga hanyoyin sammai, waxanda suke kaiwa gare shi, in ga abin bautawar Musa, wanda yake riya cewa shi ne abin bauta da gaskiya, amma fa ni ina zaton Musa qarya yake yi cikin abin da yake da'awa. Haka aka qawatawa Fir'auna mummunan aikinsa, yayin da ya nemi abin da ya nema daga Hamana, aka kawar da shi daga barin hanyar gaskiya zuwa hanyar vata. Makircin Fir'auna na xaukaka varnar da yake kai, da vata gaskiyar da Annabi Musa ya zo da ita, ba komai ba ne face asara, saboda qarshen lamarinsa shi ne tavewa da rashin cin nasara a cikin aikinsa, da tavewar da bata yankewa har abada.**

**38 Wannan mutumin da ya yi imani daga mabiya Fir'auna ya ce, yana mai nasiha ga mutanensa, yana mai shiryar da su zuwa ga hanyar gaskiya: "Ya ku mutane na, ku min biyayya, in shiryar daku in nuna muku tafarkin madaidaici, tafarkin shiriya zuwa ga gaskiya".**

**39 Ya ku mutane na, wannan rayuwar ta duniya ba komai bace face jin daxi da kayan daxi masu yankewa, don haka kada ta ruxe ku da abin da yake cikinta na jin daxi mai yankewa, kuma gidan lahira da abin da yake cikinta na ni'ima madauwamiya, wadda bata yankewa, ita ce gidan tabbata da zama, don haka ku yi aiki saboda wannan rana ta hanyar xa'ar Allah, kuma ku kiyayi shagalta da rayuwarku ta duniya, da barin aiki don lahira.**

**40 Duk wanda ya yi mummunan aiki, to ba za a yi masa uquba ba sai da irin abin da ya aikata, ba za a qara masa uquba ba. Wanda ya yi aiki na qwarai, yana neman yardar Allah da shi, namiji ne mai aikin ko mace, kuma yana mai imani da Allah da Manzanninsa, to waxanda suka siffatu da waxannan siffofi masu kyau za su shiga Aljannah a ranar alqiyama, kuma Allah yana azurta su da abin da ya tanada a cikinta na yayan itatuwa, da ni'ima daumammmiya wadda bata yankewa har abada, ba tare da lissafi ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin jayayya don vata gaskiya da tabbatar da vata, xabi'a ce mummuna, kuma yana cikin siffofin vatattu.**
**2 - Girman kai yana hana shiriya ga gaskiya.**
**3 - Dabarun kafirai na vata gaskiya da makircinsu a banza suke qarewa.**
**4 - Wajabcin tanadi domin ranar alqiyama, da rashin shagaltuwa da duniya da barinta.**

الحِزْبُ ٤٨

۞ وَيَٰقَوۡمِ مَا لِيٓ أَدۡعُوكُمۡ إِلَى ٱلنَّجَوٰةِ وَتَدۡعُونَنِيٓ إِلَى ٱلنَّارِ ٤١
تَدۡعُونَنِي لِأَكۡفُرَ بِٱللَّهِ وَأُشۡرِكَ بِهِۦ مَا لَيۡسَ لِي بِهِۦ
عِلۡمٞ وَأَنَا۠ أَدۡعُوكُمۡ إِلَى ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡغَفَّٰرِ ٤٢ لَا جَرَمَ أَنَّمَا
تَدۡعُونَنِيٓ إِلَيۡهِ لَيۡسَ لَهُۥ دَعۡوَةٞ فِي ٱلدُّنۡيَا وَلَا فِي ٱلۡأٓخِرَةِ
وَأَنَّ مَرَدَّنَآ إِلَى ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ ٤٣
فَسَتَذۡكُرُونَ مَآ أَقُولُ لَكُمۡۚ وَأُفَوِّضُ أَمۡرِيٓ إِلَى ٱللَّهِۚ
إِنَّ ٱللَّهَ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ٤٤ فَوَقَىٰهُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِ مَا مَكَرُواْۖ
وَحَاقَ بِـَٔالِ فِرۡعَوۡنَ سُوٓءُ ٱلۡعَذَابِ ٤٥ ٱلنَّارُ يُعۡرَضُونَ
عَلَيۡهَا غُدُوّٗا وَعَشِيّٗاۚ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ أَدۡخِلُوٓاْ ءَالَ
فِرۡعَوۡنَ أَشَدَّ ٱلۡعَذَابِ ٤٦ وَإِذۡ يَتَحَآجُّونَ فِي ٱلنَّارِ
فَيَقُولُ ٱلضُّعَفَٰٓؤُاْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ إِنَّا كُنَّا لَكُمۡ
تَبَعٗا فَهَلۡ أَنتُم مُّغۡنُونَ عَنَّا نَصِيبٗا مِّنَ ٱلنَّارِ ٤٧ قَالَ
ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ إِنَّا كُلّٞ فِيهَآ إِنَّ ٱللَّهَ قَدۡ حَكَمَ
بَيۡنَ ٱلۡعِبَادِ ٤٨ وَقَالَ ٱلَّذِينَ فِي ٱلنَّارِ لِخَزَنَةِ جَهَنَّمَ
ٱدۡعُواْ رَبَّكُمۡ يُخَفِّفۡ عَنَّا يَوۡمٗا مِّنَ ٱلۡعَذَابِ ٤٩



(41) Ya ku mutane na me yasa ina kiranku zuwa ga kuvuta daga asara a rayuwar duniya da lahira, ta hanyar imani da Allah da aiki nagari, amma ku kuna kira na zuwa ga shiga wuta, da abin da kuke kira na zuwa gare ni, na kafirce wa Allah da sava masa?.

(42) Kuna kirana ga vatanku domin burin in kafirce wa Allah, kuma in bautawa waninsa tare da shi, wanda bani da wani ilimi da ke tabbatar da ingancin bautar wanin Allah, ni kuma ina kiran ku ne zuwa ga imani da Allah Mabuwayi, wanda ba a yin galaba a kansa, mai yawan gafara ga bayinsa.

(43) Gaskiya ne abin da kuke kira na zuwa ga imani da shi da yi masa xa'a, bashi da wata cancantar a kirawo shi a duniya ko a lahira, kuma baya amsa kiran wanda ya kirawo shi, kuma makomar mu gaba xaya tana ga Allah shi kaxai, sannan waxanda suka zurfafa cikin kafirci da savon Allah su ne 'yan wuta, waxanda za su lazimci shigarta a ranar alqiyama.

(44) Sai suka qi karvar nasihar sa, sai ya ce da su: "Nan gaba zaku tuna abin da na gabatar muku na nasiha, ku yi da na sani a kan qin karvar sa, don haka na miqa al'amurana gaba xayansu ga Allah shi kaxai, haqiqa Allah babu wani abin da yake vuya a gare shi daga ayyukan bayinsa.

(45) Sai Allah ya kare shi daga mummunan makircinsu a lokacin da suka yi nufin kashe shi, azabar nutsewa a cikin teku ta mamaye mutanen Fir'auna. Haqiqa Allah ya nutsar da shi da rundunarsa gaba xaya a wannan duniya.

(46) Kuma bayan mutuwarsu za a bijiro da su ga wuta a cikin qaburburansu a farkon yini da qarshensa, ranar tashin alqiyama za a ce da su: "Ku shigar da mabiya Fir'auna a cikin mafi tsananin azaba, kuma mafi girma, saboda abin da suke kai na kafirci da qaryatawa da kangewa ga bin hanyar Allah.

(47) Ka ambata - Ya kai wannan Manzo - yayin da mabiya da waxanda aka bi daga cikin 'yan wuta suke yin jayayya, sai mabiya raunana su cewa waxanda suka bi masu girman kai: "Haqiqa mu mun kasance mabiyanku ne a kan vata a duniya, shin zaku iya xauke mana wani vangare na azabar Allah?"

(48) Sai waxanda aka bi masu girman kai su ce: "Da ku mabiyan da mu waxanda aka bin duk muna cikin wuta, kuma ba wanda zai xaukewa wani vangare na azabar lahira. Allah ya riga ya yi hukunci tsakanin bayi, ya bawa kowa abin da ya cancance shi na azaba".

(49) Waxanda ake yi musu azaba a cikin wuta daga mabiya da waxanda aka bi zasu faxawa Mala'iku, waxanda aka wakilata su kula da wuta, lokacin da suka xeve qaunar fita daga cikin wuta, da dawowa duniya don su tuba: "Ku roqa mana ubangijnku ya sauqaqa mana wannan azabar madauwamiya koda na rana xaya ne".

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Muhimmancin dogaro ga Allah.
2 - Kuvutar mai kira ga Allah daga makircin abokan gaba.
3 - Tabbatar da azabar barzahu.
4 - Yadda kafirai suke rataya da duk wani abin da zai hutar da su daga wuta, koda na xan wani lokaci ne kaxan, wannan kuma abu ne da ba zai samu ba.

قَالُوٓاْ أَوَلَمۡ تَكُ تَأۡتِيكُمۡ رُسُلُكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ قَالُواْ بَلَىٰۚ
قَالُواْ فَٱدۡعُواْۗ وَمَا دُعَٰٓؤُاْ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٍ ٥٠
إِنَّا لَنَنصُرُ رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا
وَيَوۡمَ يَقُومُ ٱلۡأَشۡهَٰدُ ٥١ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ ٱلظَّٰلِمِينَ مَعۡذِرَتُهُمۡۖ
وَلَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٥٢ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى
ٱلۡهُدَىٰ وَأَوۡرَثۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡكِتَٰبَ ٥٣ هُدٗى
وَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٥٤ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ
حَقّٞ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ بِٱلۡعَشِيِّ
وَٱلۡإِبۡكَٰرِ ٥٥ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ
بِغَيۡرِ سُلۡطَٰنٍ أَتَىٰهُمۡ إِن فِي صُدُورِهِمۡ إِلَّا كِبۡرٞ
مَّا هُم بِبَٰلِغِيهِۚ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ
ٱلۡبَصِيرُ ٥٦ لَخَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ أَكۡبَرُ مِنۡ
خَلۡقِ ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٥٧
وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَلَا ٱلۡمُسِيٓءُۚ قَلِيلٗا مَّا تَتَذَكَّرُونَ ٥٨



**(50) Sai masu tsaron wuta su faxa cikin mayar da martani ga kafirai su ce: "Shin Manzannin ku basu kasance suna zuwa muku da hujjoji da dalilai bayyanannu ba?". Sai kafirai su ce: "Tabbas sun kasance suna zuwar mana da hujjoji da dalilai bayyanannu". Sai masu tsaron su ce musu cikin gatse: "Ku roqa da kan ku, mu ba ma nemawa kafirai ceto". Addu'ar kafirai vata lokaci ne da tozartar da shi, saboda ba a karvar ta daga gare su, saboda kafircin su.**

**Yayin da Allah ya ambaci qissar Fir'auna da yadda qarshensa ya kasance, da qarshen mabiyansa a nan duniya da lahira, sai ya ambaci lamarin Manzanni da Muminai, da abin da zasu samu na nasara a duniya da lahira, ya ce:**

**(51) Tabbas mu zamu taimaki Manzannin mu da waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsu su a duniya, ta hanyar bayyana hujjarsu, da qarfafa su akan abokan gabarsu, da basu nasara a ranar alqiyama, ta hanyar shigar da su Aljannah, kuma da yi wa abokan husumar su a duniya uquba ta shigar da su wuta, bayan Mala'iku da Annabawa da Muminai sun bada shaida a kan isar da saqon Allah, da kuma qaryatawar da al'ummu suka yi.**

**(52) Ranar da waxanda suka zalunci kansu da yin kafirci da savo hanzarinsu ba ya amfanar su da komai, kuma a wannan rana suna da kora daga rahamar Allah, kuma suna mummunan gida a lahira, saboda abin da za su haxu da shi na azaba mai raxaxi.**

**(53) Haqiqa mun bawa Annabi Musa ilimin da bani Isra'ila zasu shiriya zuwa ga gaskiya da shi, muka sanya Attaura ta zama littafi ne abin gadarwa a cikin bani Isra'ila, suna gadar sa jama'a bayan jama'a.**

**(54) Don shiriya zuwa ga tafarki na gaskiya, da tunatarwa ga ma'abota lafiyayyun hankula.**

**(55) Ka yi haquri - Ya kai wannan Manzo - akan abin da kake gamuwa da shi na qaryatawar mutanenka da cutarwarsu. Tabbas alqawarin da Allah ya yi maka na samun nasara da qarfafawa gaskiya ne, babu shakka a ciki, ka nemi gafara daga zunubanka, ka tsarkake Ubangijin da godiya gare shi farkon yini da qarshensa.**

**(56) Waxanda suke yin jayayya cikin ayoyin Allah don qoqarin vata su ba tare da wata hujja ko dalili ba, ba abin da**
**yasa su yin hakan sai neman xaukaka da girman kai ga gaskiya, amma baza su tava samun abin da suke nema ba**
**na xaukaka. Don haka – Ya kai wannan Manzo – ka yi riqo da Allah, haqiqa shi mai ji ne ga maganganun bayinsa,**
**kuma mai ganin ayyukansu, babu abin da yake kuvuce masa daga cikinsu, kuma da sannu zai yi musu sakayya a**
**kansu. (57) Haqiqa halittar sammai da qassai tafi halittar mutane girma, saboda girmansu da faxinsu, to wanda ya**
**halicce su tare da girmansu da faxinsu mai iko ne a kan tayar da matattu daga qabarinsu, su dawo rayayyu, don**
**ya yi musu hisabi kuma ya saka musu, sai dai da yawa daga cikin mutane basu san hakan ba, basa xaukan izina da**
**hakan, kuma basa sanya hakan ya zama dalili a kan yiwuwar tashin alqiyama, duk da fitowarsa fili.**

**(58) Wanda baya gani ba zai yi daidai da mai gani ba, haka nan waxanda suka yi imani da Allah, suka gasgata Manzanninsa, suka kyautata ayyukansu, ba zasu tava daidaita da waxanda suke munana ayyukansu ba, ta hanyar gurvatarciyar aqida, da savon Allah, sai dai kaxan ne su ke tuna hakan, domin da a ce kuna tunawa da kun gane bambancin dake tsakanin vangarori biyun, kuma da kun yi qoqarin zamowa daga cikin waxanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka na qwari, domin kwaxayin samun yardar Allah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Taimakon Allah ga Manzanni da Muminai sunnace ta Allah tabbatacciya. 2 - Hanzarin da azzalumi zai gabatar a ranar alqiyama ba zai yi masa amfani ba. 3 - Muhimmancin haquri wurin tunkarar varna. 4 - Sammai da qasa suna tabbatar da yiwuwar tashin alqiyama, domin wanda ya iya halittar babban abu, to mai iko ne a kan ya dawo da rayuwar abin da bai kai shi ba.**

إِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَأٓتِيَةٞ لَّا رَيۡبَ فِيهَا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ
لَا يُؤۡمِنُونَ ٥٩ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ
دَاخِرِينَ ٦٠ ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ لِتَسۡكُنُواْ
فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ
أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ ٦١ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ
خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٦٢
كَذَٰلِكَ يُؤۡفَكُ ٱلَّذِينَ كَانُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٦٣
ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ قَرَارٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ
وَصَوَّرَكُمۡ فَأَحۡسَنَ صُوَرَكُمۡ وَرَزَقَكُم مِّنَ
ٱلطَّيِّبَٰتِۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡۖ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ
ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٤ هُوَ ٱلۡحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ
لَهُ ٱلدِّينَۗ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٥ ۞ قُلۡ إِنِّي (ربع الحزب ٤٨)
نُهِيتُ أَنۡ أَعۡبُدَ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَمَّا جَآءَنِيَ
ٱلۡبَيِّنَٰتُ مِن رَّبِّي وَأُمِرۡتُ أَنۡ أُسۡلِمَ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٦



**(59) Haqiqa lokacin da Allah zai tashi matattu domin yi musu hisabi, da basu sakamako mai zuwa ne babu makawa, babu shakka a ciki, sai dai da yawa daga cikin mutane basu yi imani da zuwan sa ba, don haka ya sa ma basa yin shiri domin wannan rana.**

**(60) Ubangijinku ya ce – Ya ku Mutane - : “Ku kaxaita ni cikin bauta da roqo, ni kuma zan amsa muku roqonku, in yi muku afuwa, in jiqan ku. Haqiqa waxanda suke yin girman kai a kan kaxaita ni da bauta, to zasu shiga wutar Jahannama a ranar alqiyama cikin qasqanci da wulaqanci.**

**(61) Allah shi ne wanda ya sanya muku dare ya zama mai duhu, domin ku samu hutu da nutsuwa a cikinsa, kuma ya sanya yini ya zama mai haske, domin ku yin aiki a cikinsa. Haqiqa Allah ma’abocin falal ne ga mutane, yayin da ya lulluve su da ni’imominsa na zahiri da baxini, sai dai da yawa daga cikin mutane basa gode masa Maxaukakin Sarki a kan ni’imominsa.**

**(62) Wannan shi ne Allah, wanda ya yi muku baiwa da ni’imominsa, shi ne Mahaliccin dukkan komai, babu wani Mahalicci wanda ba shi ba, babu abin bautawa da gaskiya sai shi, to ta yaya ake juyar da ku daga bautarsa zuwa bautawa waninsa, wanda baya mallakar amfani ko cutarwa?.**

**(63) Kamar yadda ya juyar da waxannan daga barin imani da Allah da bauta masa shi kaxai, haka yake juyar da wanda yake jayayya da ayoyin Allah da suke nuna kaxaitakar sa a kowane lokaci da zamani, baya shiriya zuwa ga gaskiya, kuma ba a datar da shi zuwa ga shiriya.**

**(64) Allah wanda ya sanya muku qasa – Ya ku Mutane - ta zama wani waje shiryayye don ku samu matabbata a kanta, ya sanya sama ta zama gini mai inganci a saman ku, wadda aka kare daga faxowa, kuma ya suranta ku a cikin cikin iyayenku mata, ya kyautata surarku, kuma ya azurta ku daga daxaxan abubuwan ci na halal. Wanda ya yi muku waxannan ni’imomi shi ne Allah Ubangijinku. Albarkar Allah Ubangijin talikai gaba xaya ta yawaita, ba su da wani Ubangiji wanda ba shi ba.**

**(65) Shi ne rayayyen da baya mutuwa, kuma babu wani abin bauta da gaskiya wanda ba shi ba, ku kira shi da bauta ko da roqo, ku masu nufin shi, shi kaxai, kada ku haxa shi da wani a cikin halittarsa. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin dukkan halittu.**

**(66) Ka ce - Ya kai wannan Manzo: “Haqiqa ni Allah ya hana ni na bautawa waxanda kuke bautawa koma bayan Allah, na daga gumaka, waxanda basa amfanarwa, kuma basa cutarwa, lokacin da hujjoji da dalilai bayyanannu suka zo min akan vacin bautarsu, kuma Allah ya umarce ni na jayu gare shi, shi kaxai da yi masa bauta, shi ne Ubangijin halitta baki xaya,. Bata da wani Ubangiji wanda ba shi ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Roqon Allah yana cikin ma’anonin bautar Allah, wadda ba juyar da ita sai ga Allah, saboda addu’a ita ce haqiqanin bautar Allah.**

**2 - Ni’imomin da Allah ya yi suna wajabta a gode masa.**

**3 - Tabbatuwar sifar rayuwa ga Allah.**

**4 - Muhimmancin tsarke niyya a cikin aiki.**

هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ مِنۡ عَلَقَةٖ ثُمَّ
يُخۡرِجُكُمۡ طِفۡلٗا ثُمَّ لِتَبۡلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمۡ ثُمَّ لِتَكُونُواْ شُيُوخٗاۚ
وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ مِن قَبۡلُۖ وَلِتَبۡلُغُوٓاْ أَجَلٗا مُّسَمّٗى وَلَعَلَّكُمۡ
تَعۡقِلُونَ ٦٧ هُوَ ٱلَّذِي يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ فَإِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا
يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٦٨ أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ
فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ أَنَّىٰ يُصۡرَفُونَ ٦٩ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِٱلۡكِتَٰبِ
وَبِمَآ أَرۡسَلۡنَا بِهِۦ رُسُلَنَاۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٧٠ إِذِ ٱلۡأَغۡلَٰلُ
فِيٓ أَعۡنَٰقِهِمۡ وَٱلسَّلَٰسِلُ يُسۡحَبُونَ ٧١ فِي ٱلۡحَمِيمِ
ثُمَّ فِي ٱلنَّارِ يُسۡجَرُونَ ٧٢ ثُمَّ قِيلَ لَهُمۡ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ
تُشۡرِكُونَ ٧٣ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا بَل لَّمۡ نَكُن
نَّدۡعُواْ مِن قَبۡلُ شَيۡـٔٗاۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٤
ذَٰلِكُم بِمَا كُنتُمۡ تَفۡرَحُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَبِمَا كُنتُمۡ
تَمۡرَحُونَ ٧٥ ٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئۡسَ مَثۡوَى
ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ٧٦ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۚ فَإِمَّا نُرِيَنَّكَ
بَعۡضَ ٱلَّذِي نَعِدُهُمۡ أَوۡ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِلَيۡنَا يُرۡجَعُونَ ٧٧



**(67) Shi ne ya halicci babanku Annabi Adam daga turvaya, sannan ya sanya halittarku a bayansa daga xigon maniyyi, sannan bayan xigon maniyyin daga daskararren jini, sannan bayan haka sai ya fitar da ku daga cikin mahaifanku kuna jarirai qanana, sannan sai ku iso zuwa ga shekarun da jikinku zai yi qarfi, sannan sai ku girma ku zamo tsofaffi. Daga cikinku akwai waxanda suke mutuwa gabanin hakan, kuma don ku kai wani lokaci iyakantacce a wurin Allah, ba zaku rage ba, kuma ba zaku qara ba, kuma ko wataqila ku amfana da wannan hujjoji da dalilai a kan ikon Allah da kaxaitakarsa.**

**(68) Allah shi kaxai shi ne wanda rayawa take a hannunsa, shi ne shi kaxai kashewa take a hannunsa. Idan ya nufi wani abu ya kasance, kawai zai cewa wannan lamari: "kasance, sai ya kasance".**

**(69) Ya kai wannan Manzo, shin baka ga waxanda suke yin jayayya a cikin ayoyin Allah ba, suna masu qaryatawa da su, duk da fitowarsu a fili. Ka yi mamakin halinsu, suna bijirewa gaskiya duk da fitowarta fili.**

**(70) Waxanda su ka qaryata Alqur'ani, da abin da muka aiko Manzannin mu da shi na gaskiya, da sannu waxannan masu qaryatawar zasu san qarshen qaryatawar su, kuma zasu ga mummunan qarshe.**

**(71) Zasu san qarshen lamarin yayin da sasari zai kasance a wuyansu, sarqoqi kuma a qafafunsu, Mala'ikun wuta (Zabaniyawa) suna jan su.**

**(72) Ana jan su a cikin ruwan zafi mai tsananin tafasa, sannan a cikin wuta za a cinna su, su zama makamashi.**

**(73) Sannan a ce da su cikin wulaqantarwa da tsawatarwa: "Ina allolin da kuke riyawa, waxanda kuka haxa Allah da su wajen bauta?".**

**(74) Koma bayan Allah, daga gumakan ku waxanda basa amfanarwa, basa cutarwa?. Sai Kafirai su ce: "Sun vace mana bama ganin su, kai! mu a duniya bama bautawa wani abu da ya cancanta a bauta masa. To kamar yadda waxannan suka vacewa gaskiya, haka Allah yake vatar da kafirai ga barin gaskiya, a kowane wuri da zamani.**

**(75) Za a ce da su: "Wannan azabar da kuke xanxanar ta saboda farin cikin da kuke yi a kan abin da kuke kai na shirka, da yalwatawar ku a cikin farin ciki.**

**(76) Ku shiga qofofin wutar Jahannama, kuna masu zama a cikinta har abada. Matabbatar masu yin girman kai ta munana.**

**Yayin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya sha wahalar da ya sha da mutanensa, sai Allah ya umarce shi da yin haquri, kuma ya kwantar masa da hankali ta hanyar yi masa alqawarin samun nasara, sai ya ce:**

**(77) Ka yi haquri - Ya kai wannan Manzo - game da cutarwar mutanenka da qaryatawar su, tabbas alqawarin da Allah ya yi maka na taimakonka gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa. Ko dai mu nuna maka wani vangare na alqawarin mu na azaba a kansu, a cikin rayuwarka wannan, kamar yadda ya faru a yaqin badar, ko kuma mu karve ka gabanin hakan, to gare mu ne kaxai zasu koma ranar alqiyama, sai mu saka musu a kan ayyukansu, mu shigar da su wuta, suna masu dauwama a cikinta har abada.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sannu sannu cikin yin halitta sunnar Allah ce, kuma ya kamata mutane su koyi bi a sannu sannu a cikin rayuwarsu. 2 - Munin yin farin ciki da vata.**

**3 - Muhimmancin haquri a cikin rayuwar mutane, Musamman masu kira zuwa ga Allah.**

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلٗا مِّن قَبۡلِكَ مِنۡهُم مَّن قَصَصۡنَا عَلَيۡكَ
وَمِنۡهُم مَّن لَّمۡ نَقۡصُصۡ عَلَيۡكَۗ وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ أَن يَأۡتِيَ
بِـَٔايَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ فَإِذَا جَآءَ أَمۡرُ ٱللَّهِ قُضِيَ بِٱلۡحَقِّ وَخَسِرَ
هُنَالِكَ ٱلۡمُبۡطِلُونَ ٧٨ ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَنۡعَٰمَ
لِتَرۡكَبُواْ مِنۡهَا وَمِنۡهَا تَأۡكُلُونَ ٧٩ وَلَكُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ
وَلِتَبۡلُغُواْ عَلَيۡهَا حَاجَةٗ فِي صُدُورِكُمۡ وَعَلَيۡهَا وَعَلَى
ٱلۡفُلۡكِ تُحۡمَلُونَ ٨٠ وَيُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ فَأَيَّ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ
تُنكِرُونَ ٨١ أَفَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ
كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ أَكۡثَرَ مِنۡهُمۡ وَأَشَدَّ
قُوَّةٗ وَءَاثَارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ
٨٢ فَلَمَّا جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَرِحُواْ بِمَا عِندَهُم مِّنَ
ٱلۡعِلۡمِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٨٣ فَلَمَّا رَأَوۡاْ
بَأۡسَنَا قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَحۡدَهُۥ وَكَفَرۡنَا بِمَا كُنَّا بِهِۦ
مُشۡرِكِينَ ٨٤ فَلَمۡ يَكُ يَنفَعُهُمۡ إِيمَٰنُهُمۡ لَمَّا رَأَوۡاْ بَأۡسَنَاۖ سُنَّتَ
ٱللَّهِ ٱلَّتِي قَدۡ خَلَتۡ فِي عِبَادِهِۦۖ وَخَسِرَ هُنَالِكَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٥



**(78) Haqiqa mun aiko Manzanni da yawa gabaninka – Ya kai wannan Manzo - zuwa ga al'ummunsu, amma sai suka qaryata su, suka cutar da su, sai Manzannin suka yi haquri akan qaryata su da cutar da su. Daga cikin Waxannan Manzannin akwai waxanda muka baka labarinsu, daga cikinsu akwai waxanda bamu baka labarinsu ba, baya yiwuwa ga wani Manzo ya zowa mutanensa da wata aya daga Ubangijinsa sai da ganin damar Allah, don haka shawarar kafirai ga al'ummunsu a kan su zo musu da ayoyi zalunci ne, idan lamarin Allah ya zo da buxi, ko raba gari tsakanin Manzanni da mutanensu, to sai ya rabe tsakaninsu da adalci, a halakar da kafirai, a tseratar da Manzanni, kuma a wannan matsayi ne – da ake rarrabewa tsakanin bayi - ma'abota vatanci zasu yi asarar kansu, ta hanyar kai ta ga halaka saboda kafircin su.**

**(79) Allah shi ne wanda ya sanya muku raquma da shanu da tumaki, domin ku hau wasu daga ciki, kuma ku ci naman wasu daga ciki.**

**(80) Kuma kuna da amfani mai yawa a cikin waxannan dabbobi, amfanin da yake sabunta a kowane zamani, kuma kuna samun abin da ranku yake so daga dabbobin na buqatu, mafi bayyanar buqatunku da kuke yi da su shi kai-kawo a tudu da teku.**

**(81) Kuma Allah mai tsarki yana nuna muku daga ayoyinsa waxanda suke nuna ikonsa da kaxaitakarsa, to wanne ne a cikin ayoyin Allah baku yarda da su ba, bayan ya tabbata a gare ku cewa su ayoyin Allah ne?.**

**(82) Waxannan masu qaryatawa basu tafiya ba ne a bayan qasa?, su lura yaya qarshen al'ummun da suka qaryata gabaninsu ya kasance, sai xau izina daga gare su?. Haqiqa waxancan al'ummu sun fi waxannan dukiya, da tsananin qarfi, da yawan raya gurabe a bayan qasa. Amma abin da suke da shi na qarfi bai wadata musu komai ba, yayin da azabar Allah mai halakarwa ta zo musu.**

**(83) Yayin da Manzanninsu suka zo musu da hujjoji da dalilai bayyanannu, sai suka qaryata su, suka yarda da riqon abin da yake wajensu na ilimi wanda ya ci karo da abin da Manzannin suka zo musu da shi, kuma abin da suke yin izgili da shi na azaba ya sauka a kansu, wanda Manzanni suke tsoratar da su shi.**

**(84) Yayin da suka ga azabar mu sai suka ce suna masu tabbatar da abin da ake faxa musu, a lokacin da tabbatarwar bata amfani: "Mun yi imani da Allah shi kaxai, mun kafirce wa waxanda muke bautawa koma bayan Allah, daga gumaka da abokan tarayya".**

**(85) Imanin su bai kasance mai amfani a gare su ba a yayin da suka yi ido biyu da azabar mu tana sauka a kansu, haka tsarin Allah yake game da bayinsa da suka gabata, imaninsu yayin da suka ga azaba baya amfani. Kafirai sun yi asara lokacin da azaba ta sauka a kansu domin sun kai kawunansu cikin halaka, saboda kafircewa Allah da rashin tuba tun kafin ganin azaba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah yana da Manzanni, bayan waxanda ya ambata a cikin Alqur'ani mai girma, kuma ya wajaba mu yi imani da su a dunqule.**

**2 - Yana daga cikin ni'imomin Allah, bayyana ayoyi masu nuna kaxaitakar sa.**

**3 - Haxarin yin fariya da vata, da mummunan qarshen ma'abocin haka.**

**4 - Imani yayin da aka ga azaba mai halakarwa vatacce.**

ترتيبها ٤١ سُورَةُ فُصِّلَتْ آياتها ٥٤

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ١ تَنزِيلٞ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٢ كِتَٰبٞ فُصِّلَتۡ ءَايَٰتُهُۥ
قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا لِّقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٣ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗا فَأَعۡرَضَ أَكۡثَرُهُمۡ
فَهُمۡ لَا يَسۡمَعُونَ ٤ وَقَالُواْ قُلُوبُنَا فِيٓ أَكِنَّةٖ مِّمَّا تَدۡعُونَآ إِلَيۡهِ
وَفِيٓ ءَاذَانِنَا وَقۡرٞ وَمِنۢ بَيۡنِنَا وَبَيۡنِكَ حِجَابٞ فَٱعۡمَلۡ إِنَّنَا عَٰمِلُونَ
٥ قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ
فَٱسۡتَقِيمُوٓاْ إِلَيۡهِ وَٱسۡتَغۡفِرُوهُۗ وَوَيۡلٞ لِّلۡمُشۡرِكِينَ ٦ ٱلَّذِينَ
لَا يُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٧ إِنَّ ٱلَّذِينَ
نصف الحزب ٤٨ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٨ ۞ قُلۡ أَئِنَّكُمۡ
لَتَكۡفُرُونَ بِٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ فِي يَوۡمَيۡنِ وَتَجۡعَلُونَ لَهُۥٓ أَندَادٗاۚ
ذَٰلِكَ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٩ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ مِن فَوۡقِهَا
وَبَٰرَكَ فِيهَا وَقَدَّرَ فِيهَآ أَقۡوَٰتَهَا فِيٓ أَرۡبَعَةِ أَيَّامٖ سَوَآءٗ
لِّلسَّآئِلِينَ ١٠ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ وَهِيَ دُخَانٞ فَقَالَ
لَهَا وَلِلۡأَرۡضِ ٱئۡتِيَا طَوۡعًا أَوۡ كَرۡهٗا قَالَتَآ أَتَيۡنَا طَآئِعِينَ ١١



# Suratu Fussilat

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin hanyar gamsar da masu bijirewa Alqur'ani a cikin tausasawa, ta hanyar bayyana musu cewa Alqur'ani gaskiya ne, da bayanin mummunan qarshen bijirewa.**

## Tafsir:

**1 (Haa Mim) Bayani a kan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqara.**

**2 Wannan Alqur'ani abin saukarwa ne daga Allah mai rahama mai jinqai.**

**3 Littafi ne da aka yi bayanin ayoyinsa, cikakken bayani kammalalle. Kuma aka sanya shi abin karantawa (Alqur'ani) da harshen larabci ga mutanen da suke ganewa, domin su ne suke amfanuwa da ma'anoninsa, da abin da yake cikinsa na shiriya zuwa ga gaskiya.**

**4 Kuma yana yin bushara ga Muminai da tanadin da ya yi musu na sakamako mai yawa, kuma yana tsoratar da kafirai daga azaba mai raxaxi. Amma sai mafi yawa daga cikinsu suka bijire masa, basa sauraron abin da yake cikinsa na shiriya, sauraro na karva da kuma yarda.**

**5 Suka ce: "Zukatan mu a rufe suke da abin rufewa, basa hankaltar abin da kuke kiran mu zuwa gare shi, kuma a cikin kunnuwanmu akwai kurumta, basa jin sa, sannan a tsakanin mu da kai akwai shamaki, don haka abin da kake faxa baya ya isowa gare mu, saboda haka ka yi aiki a kan tsarinka, muma zamu yi aiki a kan namu tsarin, ba zamu bika ba.**

**6 Ya kai wannan Manzo ka faxawa waxannan masu taurin kai ka ce: "Ni mutum ne kamar ku, ana yi min wahayi cewa: abin bautar ku bisa cancanta abin bauta ne guda xaya, shi ne Allah, don haka ku bi hanyar da zata kai ku zuwa gare shi, ku nemi gafarar zunubanku daga gare shi, halaka da azaba ta tabbata ga mushrikan da suke bautawa wanin Allah, ko suke haxa wani da shi a wajen bauta.**

**7 Waxanda basa bada zakkar dukiyoyin su, kuma sun kafircewa lahira da abin da yake cikinta na ni'ima dauwamammiya, da azaba mai raxaxi.**

**8 Haqiqa waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma suka yi ayyuka nagari, suna wani lada dauwamamme wanda baya yankewa, shi ne Aljannah.**

**9 Ya kai wannan Manzo kace – kana mai tsawatar wa ga mushirikai: "Saboda me kuke kafirce wa Allah, wanda ya halicci qasa a kwana biyu: ranar lahadi da litinin, kuna sanya masa kishiyoyi da kuke bauta musu koma bayan Allah?. Alhali shi ne Ubangijin dukkan halitta gaba xaya.**

**10 Kuma ya sanya tabbatattun duwatsu a samanta, waxanda suke riqe da ita, domin kada ta motsa, ya qaddara abincin mutane da dabbobi a cikin kwanaki huxu, idan aka haxa da waxancan kwanaki biyun da suka gabata, su ne talata, da laraba, koda wani zai so ya yi tambaya a kan hakan.**

**11 Sannan Allah (S.W.T) ya nufi halittar sama, a wannan lokacin tana hayaqi, sai yace mata, ita da qasa: "Ku yi biyayya ga umarni na, kuna son hakan, ko ba kwa so, baku da yadda zaku kaucewa hakan". sai suka ce: "Mun zo muna masu miqa wuya, bamu da wani nufi koma bayan nufin ka ya Ubangijin mu".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Irin yadda kafirai suka lalata hanyoyin da zasu shiriya da su, hakan yana nuna zasu wanzu a kan kafirci.**
**2 - Bayanin matsayin zakkah, kuma ita rukuni ce daga cikin rukunan musulunci.**
**3 - Bayanin yadda duniya da abin da yake cikinta suka miqa wuya ga lamarin Allah (S.W.T).**

فَقَضَىٰهُنَّ سَبْعَ سَمَٰوَاتٍ فِي يَوْمَيْنِ وَأَوْحَىٰ فِي كُلِّ سَمَآءٍ أَمْرَهَاۚ
وَزَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنْيَا بِمَصَٰبِيحَ وَحِفْظًاۚ ذَٰلِكَ تَقْدِيرُ ٱلْعَزِيزِ
ٱلْعَلِيمِ ﴿١٢﴾ فَإِنْ أَعْرَضُواْ فَقُلْ أَنذَرْتُكُمْ صَٰعِقَةً مِّثْلَ صَٰعِقَةِ
عَادٍ وَثَمُودَ ﴿١٣﴾ إِذْ جَآءَتْهُمُ ٱلرُّسُلُ مِنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ وَمِنْ
خَلْفِهِمْ أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَۖ قَالُواْ لَوْ شَآءَ رَبُّنَا لَأَنزَلَ مَلَٰٓئِكَةً
فَإِنَّا بِمَآ أُرْسِلْتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿١٤﴾ فَأَمَّا عَادٌ فَٱسْتَكْبَرُواْ فِي
ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَقَالُواْ مَنْ أَشَدُّ مِنَّا قُوَّةًۖ أَوَلَمْ يَرَوْاْ أَنَّ ٱللَّهَ
ٱلَّذِي خَلَقَهُمْ هُوَ أَشَدُّ مِنْهُمْ قُوَّةًۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجْحَدُونَ
﴿١٥﴾ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا صَرْصَرًا فِيٓ أَيَّامٍ نَّحِسَاتٍ لِّنُذِيقَهُمْ
عَذَابَ ٱلْخِزْيِ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَاۖ وَلَعَذَابُ ٱلْأٓخِرَةِ أَخْزَىٰۖ وَهُمْ
لَا يُنصَرُونَ ﴿١٦﴾ وَأَمَّا ثَمُودُ فَهَدَيْنَٰهُمْ فَٱسْتَحَبُّواْ ٱلْعَمَىٰ عَلَى
ٱلْهُدَىٰ فَأَخَذَتْهُمْ صَٰعِقَةُ ٱلْعَذَابِ ٱلْهُونِ بِمَا كَانُواْ يَكْسِبُونَ
﴿١٧﴾ وَنَجَّيْنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ﴿١٨﴾ وَيَوْمَ يُحْشَرُ أَعْدَآءُ ٱللَّهِ
إِلَى ٱلنَّارِ فَهُمْ يُوزَعُونَ ﴿١٩﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا مَا جَآءُوهَا شَهِدَ عَلَيْهِمْ
سَمْعُهُمْ وَأَبْصَٰرُهُمْ وَجُلُودُهُم بِمَا كَانُواْ يَعْمَلُونَ ﴿٢٠﴾



**(12) Sai Allah ya cika halittar sammai a cikin kwana biyu: ranar alhamis da Juma'a, da waxannan kwana biyun ne halittar sammai da qassai ta cika a cikin kwana shida. Allah ya yi wahayi a kowace sama abin da ya qaddara a cikinta, da abin da ya yi umarni da shi na na xa'a da bauta. Muka qawata saman duniya da taurari, kuma muka kiyaye ita saman daga satar jin da Shaixanu suke yi da waxannan taurarin. Wannan abin da aka ambata tsari ne na Allah Mabuwayi, wanda babu mai rinjayar sa, kuma masanin halittarsa.**

**(13) Idan waxannan suka bijire ga barin yin imani da abin da ka zo da shi, to ka ce da su: "Ina tsoratar da ku azabar da zata zo muku, irin wadda ta afkawa Adawa, mutanen Annabi Hud, da Samudawa mutanen Annabi Salihu, a lokacin da suka qaryata su".**

**(14) Lokacin da Manzanninsu suka zo musu, sashensu na bin sashe, da kira iri xaya, suna umartar su kada su bautawa kowa sai Allah shi kaxai. Sai kafirai daga cikinsu suka ce: "Da ubangijin mu ya so ya saukar mana da Mala'iku a matsayin Manzanni gare mu da ya saukar da su, don haka mun kafirce wa abin da aka aiko ku da shi, saboda ku mutane ne kamar mu".**

**(15) Amma Adawa mutanen Annabi Hudu bayan kafirce wa Allah da suka yi, sai suka yi girman kai ba tare da haqqi ba, suka zalunci waxanda suke kewaye da su, suka ce – suna masu yaudaruwa da qarfinsu -: "Waye ya kai mu qarfi?!, babu wanda ya kai su tsananin qarfi a tunaninsu. Sai Allah ya mayar musu da martani inda ya ce: "Shin waxannan basa gani ne, kuma basu san Allah da ya halicce su, ya sanya musu qarfin da ya ruxe su, ya fi su qarfi ba?". Sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah waxanda Annabi Hudu ya zo da su.**

**(16) Sai muka tura musu iska mai sautin da yake tsoratarwa, a wasu kwanaki marasa daxi, saboda abin da yake cikinsu na azaba, don mu xanxana musu azabar qasqanci da wulaqanci a duniya, kuma azabar lahira da take jiransu ta fi wannan qasqanci gare su, kuma baza su samu wanda zai taimake su ba ya tseratar da su daga azaba.**

**(17) Amma Samudawa mutanen Annabi Salihu haqiqa mun shiryar da su, ta hanyar bayyana musu hanyar gaskiya, amma sai suka fifita vata a kan shiriya zuwa ga gaskiya, su ma sai azaba mai qasqantarwa ta kama su, saboda abin da suke aikatawa na kafirci da savon Allah.**

**(18) Sai muka tseratar da waxanda suka yi imani da Allah da Manzannin sa, kuma suka kasance suna tsoron Allah, ta hanyar aikata umarni da nisantar hani, mun tseratar da su daga azabar da ta samu mutanensu.**

**(19) Ranar da Allah zai tattara maqiyansa zuwa ga wuta, Zabaniyawa suna haxa na farkon su da na qarshen su, a wannan rana ba zasu iya guduwa daga wuta ba.**

**(20) Har sai sun zo kusa da wutar da aka koro su zuwa gare ta, sai su yi musun abin da suka kasance suna aikatawa a duniya, sai jin su, da ganin su da fatun jikinsu su bada shaida a kan abin da suka kasance suna aikatawa a duniya na kafirci da savon Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Bijirewa gaskiya sababi ne na halaka a duniya da lahira.**
**2 - Girman kai da ruxuwa da qarfi, suna hana karvar gaskiya.**
**3 - Ana haxawa kafirai azabar lahira da ta duniya.**
**4 - Gavvai zasu yi shaida ga ma'abotansu a ranar tashin alqiyama.**

وَقَالُواْ لِجُلُودِهِمۡ لِمَ شَهِدتُّمۡ عَلَيۡنَاۖ قَالُوٓاْ أَنطَقَنَا ٱللَّهُ ٱلَّذِيٓ
أَنطَقَ كُلَّ شَيۡءٖ وَهُوَ خَلَقَكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٢١
وَمَا كُنتُمۡ تَسۡتَتِرُونَ أَن يَشۡهَدَ عَلَيۡكُمۡ سَمۡعُكُمۡ وَلَآ أَبۡصَٰرُكُمۡ
وَلَا جُلُودُكُمۡ وَلَٰكِن ظَنَنتُمۡ أَنَّ ٱللَّهَ لَا يَعۡلَمُ كَثِيرٗا مِّمَّا تَعۡمَلُونَ
٢٢ وَذَٰلِكُمۡ ظَنُّكُمُ ٱلَّذِي ظَنَنتُم بِرَبِّكُمۡ أَرۡدَىٰكُمۡ فَأَصۡبَحۡتُم
مِّنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٢٣ فَإِن يَصۡبِرُواْ فَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡۖ وَإِن يَسۡتَعۡتِبُواْ
فَمَا هُم مِّنَ ٱلۡمُعۡتَبِينَ ٢٤ ۞ وَقَيَّضۡنَا لَهُمۡ قُرَنَآءَ فَزَيَّنُواْ لَهُم
مَّا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡ وَحَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلُ فِيٓ أُمَمٖ قَدۡ
خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ خَٰسِرِينَ ٢٥
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَسۡمَعُواْ لِهَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ وَٱلۡغَوۡاْ فِيهِ
لَعَلَّكُمۡ تَغۡلِبُونَ ٢٦ فَلَنُذِيقَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَذَابٗا شَدِيدٗا
وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَسۡوَأَ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٧ ذَٰلِكَ جَزَآءُ أَعۡدَآءِ ٱللَّهِ
ٱلنَّارُۖ لَهُمۡ فِيهَا دَارُ ٱلۡخُلۡدِ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ
٢٨ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ رَبَّنَآ أَرِنَا ٱلَّذَيۡنِ أَضَلَّانَا مِنَ ٱلۡجِنِّ
وَٱلۡإِنسِ نَجۡعَلۡهُمَا تَحۡتَ أَقۡدَامِنَا لِيَكُونَا مِنَ ٱلۡأَسۡفَلِينَ ٢٩

ثلاثة أرباع الحزب ٤٨



(21) Sai kafirai su cewa fatunsu: “Don me kuka bada shaida a kanmu da abin da muka kasance muna aikatawa a duniya?”. Sai fatun su maida jawabi ga ma’abotansu su ce: “Allah wanda ya bawa komai damar yin magana shi ne ya bamu dama muka yi magana, kuma shi ne wanda ya halicce ku da farko a yayin da kuke duniya, kuma gare shi ne kaxai zaku koma a lahira, don yi muku hisabi da sakamako”.

(22) Kuma baku kasance kuna voyewa ba, a lokacin da kuke yin savon Allah a duniya, yadda jin ku da ganin ku da fatunku baza su yi muku shaida ba, saboda ku ba ku yi imani da hisabi, ko uqubar Allah, ko ladan Allah bayan mutuwa ba, kai kun yi ma zaton Allah bai san da yawa daga cikin abin da kuka kasance kuna aikatawa ba, kuna ganin ma abin ya vuya a gare shi, don haka kuka ruxu.

(23) To wannan mummunan zaton da kuka yi wa Ubangijinku shi ne ya halakar da ku, don haka kuka wayi gari kuna cikin asararru, waxanda suka yi asarar duniya da lahira.

(24) Idan waxannan, waxanda jin su da ganin su da fatun su suka yi musu shaida zasu yi haquri, to wuta ce dai matabbatar su, kuma makomar da zasu koma gare ta, kuma idan zasu nemi a yaye musu azaba, kuma su samu yardar Allah, to ba zasu samu yardar Allah ba, kuma ba zasu shiga Aljannah ba.

(25) Mun horewa waxannan kafirai abokai daga Shaixanu, suna tare da su a koyaushe, sai suka qawata musu munanan ayyukan su a duniya, kuma suka qawata musu abin da yake bayansu na lahira, sai suka mantar da su tuna lahira da aiki don ita, don haka azaba ta tabbata a kansu tare da jama’ar da suka gabace su daga cikin aljannu da mutane, tabbas sun kasance asararru, ta inda suka yi asarar kansu da iyalansu ranar alqiyama, ta hanyar shiga cikin wuta.

(26) A lokacin da kafirai suka gaza tunkarar gaskiya da hujja, sai suka yi wa juna wasici da cewa: “Kada ku saurari wannan Alqur’anin da Muhammad yake karanta muku, kada ku yi biyayya ga abin da yake cikinsa, ku yi ihu, ku xaga muryoyin ku yayin da yake karanta shi, wataqila kwa yi nasara a kansa ta hakan, sai ya daina karanta shi, ya daina kira zuwa gare shi, sai mu huta da shi”.

(27) Tabbas zamu xanxana wa waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa azaba mai tsanani a ranar alqiyama. Kuma tabbas zamu sakawa musu da mafi munin abin da suka kasance suna aikatawa na shirka da savo, don uquba a gare su.

(28) Wancan sakamako da aka ambata, sakamakon maqiya Allah, waxanda suka kafirce masa, suka qaryata Manzannin sa, shi ne wuta, zasu dauwama a cikinta, ba yankewa har abada, sakamakon jayayyar su ga ayoyin Allah, da qin imani da su, duk da cewa ayoyi ne bayyanannu da qarfin hujja.

(29) Waxanda suka kafirce wa Allah suka qaryata Manzannin sa suka ce: “Ya Ubangijin mu, ka nuna mana waxannan biyun da suka vatar da mu daga aljannu da mutane, wato Iblis wanda ya farar da kafirci, kuma ya yi kira zuwa gare shi, da xan Annabi Adam, wanda ya sunna ta zubar da jini, ka nuna mana su mu sanya su a qarqashin digadigan mu, don su zamo mafiya tsananin azaba a cikin ‘yan wuta”.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Munanawa Allah zato sifa ce daga cikin sifofin kafirci.

2 - Kafirci da savon Allah su ne sababin shaixanu su samu galaba a kan mutum.

3 - Ranar lahira mabiya zasu yi burin waxanda suka bi, su zama mafi tsananin azaba.

إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ تَتَنَزَّلُ عَلَيۡهِمُ
ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ وَأَبۡشِرُواْ بِٱلۡجَنَّةِ
ٱلَّتِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٣٠ نَحۡنُ أَوۡلِيَآؤُكُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا
وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَكُمۡ فِيهَا مَا تَشۡتَهِيٓ أَنفُسُكُمۡ وَلَكُمۡ
فِيهَا مَا تَدَّعُونَ ٣١ نُزُلٗا مِّنۡ غَفُورٖ رَّحِيمٖ ٣٢ وَمَنۡ أَحۡسَنُ
قَوۡلٗا مِّمَّن دَعَآ إِلَى ٱللَّهِ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا وَقَالَ إِنَّنِي مِنَ
ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٣٣ وَلَا تَسۡتَوِي ٱلۡحَسَنَةُ وَلَا ٱلسَّيِّئَةُۚ ٱدۡفَعۡ
بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ فَإِذَا ٱلَّذِي بَيۡنَكَ وَبَيۡنَهُۥ عَدَٰوَةٞ كَأَنَّهُۥ
وَلِيٌّ حَمِيمٞ ٣٤ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ
إِلَّا ذُو حَظٍّ عَظِيمٖ ٣٥ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ نَزۡغٞ
فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٣٦ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِ
ٱلَّيۡلُ وَٱلنَّهَارُ وَٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُۚ لَا تَسۡجُدُواْ لِلشَّمۡسِ
وَلَا لِلۡقَمَرِ وَٱسۡجُدُواْۤ لِلَّهِۤ ٱلَّذِي خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمۡ
إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ٣٧ فَإِنِ ٱسۡتَكۡبَرُواْ فَٱلَّذِينَ عِندَ
رَبِّكَ يُسَبِّحُونَ لَهُۥ بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَهُمۡ لَا يَسۡـَٔمُونَ ۩ ٣٨ سَجۡدَة



**Yayin da Allah ya ambaci sakamakon maqiyansa, sai kuma ya ambaci sakamakon masoyansa ya ce:**

**(30) Haqiqa waxanda suka ce: "Ubangijin mu shi ne Allah, ba mu da wani Ubangiji wanda ba shi ba, kuma suka tsaya, suka daidaita wajen kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, Mala'iku suna sauka a gare su yayin mutuwar su, suna ce musu: "Kada ku ji tsoro mutuwa ko abin da yake bayanta, kuma kada ku yi baqin ciki a kan abin da kuka bari a bayanku na duniya, ku yi bushara da Aljannah, wadda ake yi muku alqawarinta a duniya, sakamakon imaninku da Allah da aikinku nagari.**

**(31) Mu ne masu jivintar lamarinku a duniya, haqiqa mun kasance muna daidaita ku, muna kiyaye ku, kuma mu ne masu jivintar lamarinku a lahira, jivintar mu gare ku mai xorewa ce, kuma a cikin Aljannah kuna da duk abin da zukatanku suke sha'awa, kuna da duk abin da zaku nema daga abin da kuke so.**

**(32) Arziki ne tanadajje don saukar ku, daga Ubangiji mai yawan gafarar zunuban wanda ya tuba gare shi daga cikin bayinsa, kuma mai yawan jin qai a gare su.**

**(33) Babu wanda ya fi kyan zance fiye da mai kira zuwa ga kaxaita Allah, da yin aiki da shari'arsa, kuma ya yi aiki na qwarai, da zai sa Ubangijinsa ya yarda da shi, kuma ya ce,: "Ni ina cikin masu miqa wuya da jayuwa ga Allah". Duk wanda ya yi haka ya fi dukkan mutane kyan magana.**

**(34) Aikata kyawawan ayyuka da xa'a, waxanda suke sa Allah ya yarda, basa yin daidai da aikata savo da munanan ayyuka, waxanda suke sa Allah ya yi fushi. ka rama da abu mafi kyau ga wanda ya munana maka daga cikin mutane, sai ka ga wanda gaba ke tsakaninku a da, idan ka rama munanawar sa da abu mai kyau, ya zama kamar wani xan uwa, mai tausayawa a gare ka.**

**(35) Amma ba kowa ake datar wa ga wannan xabi'a mai kyau ba, sai waxanda suka yi haquri a kan cutarwa, da abin da suke haxuwa da shi daga mutane na munanan abubuwa. Ba kowa ake datar wa ga wannan xabi'a mai kyau ba, sai ma'abocin rabo mai girma, saboda alherin da ke ciki da alfani mai yawa.**

**(36) Idan Shaixan ya yi maka wasi wasi da wani sharri a kowane lokaci, to ka yi riqo da Allah, ka koma gare shi, tabbas Shi mai ji ne ga abin da kake faxa, kuma masani ne da halin da kake ciki.**

**(37) Daga cikin ayoyin Allah da suke nuna girmansa da kaxaitakar sa, akwai dare da yini, da yadda suke bin juna, da kuma rana da wata. Ya ku mutane kada ku yi sujjada ga rana, kada ku yi sujjada ga wata, ku yi sujjada ga Allah kaxai, wanda ya halicce su, idan har shi kaxai kuke bautawa da gaskiya.**

**(38) Idan suka yi girman kai, suka bijire, suka qi yin sujjada ga Allah Mahalicci, to Mala'ikun da suke wurin Allah suna tsarkake shi, kuma suna gode masa a dare da yini gaba xaya, basa qosawa da bautarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matsayin tsayawa a kan tafarkin Allah, abu ne mai girma a wurin Allah.**

**2 - Karamar Allah ga bayinsa Muminai, da jivintar lamarinsu, da lamarin waxanda suka bari a bayansu.**

**3 - Falalar kira zuwa ga Allah, kuma shi ne mafificin aiki.**

**4 - Yin haquri a kan cutarwa, da kuma mayar da martani da mafi kyau, waxannan xabi'u guda biyu mai kira zuwa ga Allah baya wadatuwa ga barinsu.**

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا ٱلْمَآءَ
ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِىٓ أَحْيَاهَا لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ٣٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُلْحِدُونَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا لَا يَخْفَوْنَ عَلَيْنَآ ۗ أَفَمَن
يُلْقَىٰ فِى ٱلنَّارِ خَيْرٌ أَم مَّن يَأْتِىٓ ءَامِنًا يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ ٱعْمَلُوا۟ مَا شِئْتُمْ ۖ
إِنَّهُۥ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ٤٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِٱلذِّكْرِ لَمَّا جَآءَهُمْ ۖ
وَإِنَّهُۥ لَكِتَٰبٌ عَزِيزٌ ٤١ لَّا يَأْتِيهِ ٱلْبَٰطِلُ مِنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ وَلَا مِنْ
خَلْفِهِۦ ۖ تَنزِيلٌ مِّنْ حَكِيمٍ حَمِيدٍ ٤٢ مَّا يُقَالُ لَكَ إِلَّا مَا قَدْ قِيلَ
لِلرُّسُلِ مِن قَبْلِكَ ۚ إِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغْفِرَةٍ وَذُو عِقَابٍ أَلِيمٍ ٤٣
وَلَوْ جَعَلْنَٰهُ قُرْءَانًا أَعْجَمِيًّا لَّقَالُوا۟ لَوْلَا فُصِّلَتْ ءَايَٰتُهُۥٓ ۖ
ءَا۬عْجَمِىٌّ وَعَرَبِىٌّ ۗ قُلْ هُوَ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ هُدًى وَشِفَآءٌ ۖ وَٱلَّذِينَ
لَا يُؤْمِنُونَ فِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرٌ وَهُوَ عَلَيْهِمْ عَمًى ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
يُنَادَوْنَ مِن مَّكَانٍۭ بَعِيدٍ ٤٤ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ
فَٱخْتُلِفَ فِيهِ ۗ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِىَ
بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّهُمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ٤٥ مَّنْ عَمِلَ صَٰلِحًا
فَلِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَنْ أَسَآءَ فَعَلَيْهَا ۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ٤٦



**(39) Daga cikin ayoyinsa masu nuna girmansa da kaxaitakar sa, da kuma ikonsa na tayarwa bayan mutuwa shi ne: Zaka ga qasa babu tsiro a kanta, amma idan muka saukar mata da ruwan sama sai ta motsa, saboda motsin abin da ke voye a cikinta na iri, kuma kaga ta xaga, haqiqa wanda ya raya wannan qasa matacciya da fitowar tsirrai, tabbas mai iya raya matattu ne, da tashin su don yi musu hisabi da sakamako, haqiqa shi mai iko ne a kan komai, raya qasa bayan mutuwar ta ba zai gagare shi ba, ko raya matattu da tashin su daga qabarin su.**

**(40) Lallai waxanda suke karkace wa ga barin daidai a cikin ayoyin Allah, ta hanyar inkarin su, da qaryata su, da canza su, abin da suke ciki baya vuya a gare mu, mun san su. Yanzu wanda za a jefa shi a cikin wuta shi ne mafi alheri ko kuwa wanda ranar alqiyama zai zo yana amintacce daga azaba?. Ya ku mutane ku aikata abin da kuka ga dama, na alheri da sharri, haqiqa mun yi muku bayanin alheri da sharri, kuma tabbas Allah mai gani ne da duk abin da kuka aikata, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikin ayyukan ku.**

**(41) Haqiqa waxanda suka kafirce wa Alqur'ani yayin da ya zo musu daga wurin Allah, ababen azabtarwa ne ranar alqiyama. Kuma shi (Alqur'ani) littafi ne Mabuwayi wanda aka kare, babu wani mai canzawa da ya isa ya canza shi, ko wani mai juyarwa da zai iya juya shi.**

**(42) Varna bata zuwan masa ta gabansa ko ta bayansa, da ragi ko qari, ko canza ma'ana ko lafazi. Abin saukarwa ne daga Allah mai hikima a cikin halittar sa, da gudanarwar sa, da shari'ar sa, kuma abin yabo a kowane hali. Yayin da Allah ya ambaci halin masu qaryata Alqur'ani, sai ya ba wa Manzonsa haquri, ya kwantar masa da hankali, ta hanyar bayanin abin da 'yan uwansa Manzanni suka haxu da shi gabaninsa na qaryatawa, da izgilanci, da qage, ya ce: (43) Ya kai wannan Manzo, babu wani abin da za a faxa maka na qaryatawa sai abin da aka faxawa Manzanni a gabaninka na qaryatawa, don haka ka yi haquri, tabbas Ubangijinka mai gafara ne ga wanda ya tuba zuwa gare shi daga bayinsa, kuma mai uquba ne ga wanda ya zarce a kan laifukansa, bai tuba ba. (44) Kuma da mun saukar da wannan Alqur'ani ba da harshen larabci ba, da kafirai daga cikinsu sun ce: "Ina ma an bayyana ayoyinsa don mu fahimce su, yanzu Alqur'ani zai zama bada larabci ba (ba'ajame) alhali wanda ya zo da shi balarabe ne?. Ya kai wannan Manzo, ka ce waxannan: "Alqur'ani shiriya ne daga vata, kuma waraka ne daga jahilci, da abin da ya kamace shi, amma ga waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka gasgata Manzannin sa. Waxanda basa imani da Allah akwai kurumta a kunnuwansu, kuma shi ma kurma ne a gare su, basa fahimtar sa. Waxannan da aka siffanta da abin da aka ambata, kamar waxanda ake kira ne daga nesa, ta yaya zasu ji muryar mai kiransu"!. (45) Haqiqa mun bawa Annabi Musa Attaura, sai suka yi savani a cikinta, a cikinsu akwai waxanda suka yi imani da ita, kuma a cikinsu akwai waxanda suka kafirce mata, ba don alqawarin Allah na rarrabewa a tsakanin bayi a ranar alqiyama, a cikin abin da suka sava ba, da ya yi hukunci a tsakanin waxanda suka sava a Attaura, ya bayyana mai gaskiya da wanda yake kan vata, ya girmama mai gaskiya, ya wulaqanta vatacce. Haqiqa kafirai suna cikin shakku game da lamarin wannan Alqur'anin. (46) Wanda ya yi aiki na qwarai, to amfanin aikin na shi gare shi zai koma, saboda aikin wani na qwarai baya amfanar Allah da komai. Wanda ya yi mummunan aiki, to cutar aikin a kansa zata koma, domin savon wani daga cikin halittar Allah baya cutar da shi, kuma da sannu zai sakawa kowa da abin da ya kamace shi. Kuma Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - ba mai zaluntar bayinsa ba ne, ba zai rage musu lada ba, kuma ba zai qara musu zunubi ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah ya kiyaye Alqur'ani daga canzawa, ko musanyawa, Allah ya xau nauyin wannan kiyayewar, savanin littattafan da suka gabata. 2 - Yankewar hujja ko hanzari ga mushrikan larabawa bayan saukar da Alqur'ani a da yarensu. 3 - Kore zalunci ga Allah, da kuma tabbatar masa da adalci.**